# KWATANCIN AL'ADUN KACIYA A KANO NIJERIYA DA SEBHA A LIBYA

**HASSAN MAHDI JIBRIL**

**B.A. (2010)**

**SPS/14/MHA/00001**

**KUNDIN BINCIKE WANDA AKA GABATAR DOMIN CIKASA WATA QA'IDA TA SAMUN DIGIRI NA BIYU A FANNIN HAUSA (M.A. HAUSA) A SASHEN KOYAR DA HARSUNAN NIJERIYA, JAMI'AR BAYERO, KANO**

**FABRAIRU, 2018**

## DECLARATION

I hereby declare this thesis entittle "Kamanci da Bambancin Al'adun Kaciya a Garin Kano da Sebha a Libya" (Similarities and Differences of Cultural Tradition of Circumcision Between Hausawa Kanawa and People of Sebha) is the product of my own research efforts conducted in the Department of Nigerian Languages, Bayero University, Kano under the supervisoin of Dr. Murtala Garba Yakasai. All sources have been duly acknowledged and list of references. No part of this work has been presented and will not be presented for another awards of degree or certificate elsewhere.

Hassan Mahdi Jibril

SPS/14/MHA/00001

# CERTIFICATION

This is to certify that, the research work for this thesis and its subcequent preparation by Hassan Mahdi Jibril, SPS/14/MHA/00001 were carried out under by supervision.

______________________________

Dr. Murtala Garba Yakasai
Department of Nigerian Language
Bayero University, Kano
Supervisor

______________________________

Dr. Ibrahim Garba Satatima
The Head, Department of Nigerian Language
Bayero University, Kano

## APPROVAL

____________________________

Professor Muhammad Lawan Aminu

Department of African Languages,

Ahmadu Bello University, Zaria

External Examiner

____________________________

Professor Aliyu Mu'azu

Department of Nigerian Languages

Bayero University, Kano

Internal Examiner

____________________________

Dr. Murtala Garba Yakasai

Department of Nigerian Languages

Bayero University, Kano

Supervisor

____________________________

Dr. Ibrahim Garba Satatima

The Head, Department of Nigerian Language

Bayero University, Kano

## ABUBUWAN DA KE CIKI

*Declaration* : : : : : : : : *ii*
*Certification* : : : : : : : *iii*
*Approval* : : : : : : : : *iv*
*Godiya* : : : : : : : : *viii*
*Sadaukarwa* : : : : : : : *xi*
*Gabatarwa* : : : : : : : : *xii*
*Abstract* : : : : : : : : *xiv*
*Tsakure* : : : : : : : : *xv*

**BABI NA XAYA**
**1.0 SHARE FAGE : : : : : : 1**
**1.1 Dalilan Bincike : : : : : : 2**
**1.2 Manufar Wannan Bincike : : : : : 2**
**1.3 Muradun Bincike : : : : : : 2**
**1.4 Tambayoyin Bincike : : : : : 3**
**1.5 Iyakancewar Bincike : : : : : 3**
**1.6 Gudummawar Bincike : : : : : 4**

**BABI NA BIYU**
**2.0 BITAR AYYUKAN DA SUKA GABATA : : 5**
2.1 Tarihin Kano da Kanawa a Taqaice : : : 5
2.2 Taqaitaccen Tarihin Garin Sebha a Libya : : 9
2.3 Ma’anar Kaciya : : : : : : 10
2.4 Asali da Tarihin Kaciya a Duniya : : : 13
2.4.1 Tarihin Kaciya a Wajen Hausawan Kano : : 16
2.4.2 Tarihin Kaciya a Wajen Larabawa Larabawan

Garin Sebha : : : : : : 22
2.5 Bitar Ayyukan da Suka Gabata : : : : 26
2.5.1 Kundayen Bincike : : : : : : 26
2.5.2 Bugaggun Littattafai : : : : : 36
2.5.3 Muqalu da Takardun Ilimi : : : : 48

**BABI NA UKU**
**3.0 RA'I DA DABARUN GUDANAR DA BINCIKE : 51**
3.1 Ra'in da aka Xora Wannan Bincike : : : 51
3.2 Ginshiqin Bayanai : : : : : : 54
3.2.1 Ziyarar Xakunan Ajiye Littattafai : : : 55
3.2.2 Hira da Wanzamai : : : : : : 55
3.2.3 Tattaunawa da Masana da Manazarta : : : 56
3.2.4 Tattaunawa da Likitoci Masu Fixa a Asibiti : : 57
3.2.5 Tataunawa da Tsofaffi Maza da Mata : : : 58

**BABI NA HUXU**
**4.0 KAMANCI DA BAMBANCIN AL'ADUN KACIYA A BIRNIN KANO DA GARIN SEBHA A LIBYA : 60**
4.1 Al'adun Kaciya Waxanda aka Samu Kamanci a Tsakanin Hausawa Kanawa da Larabawan Sebha a Libya : : : : : : 60
4.1.1 Kaciyar Jinya : : : : : : 60
4.1.2 Adadin 'Yankaciya : : : : : 61
4.1.3 Waqoqin Bikin Kaciya : : : : : 63
4.1.4 Masu yin Kaciya Gargajiya a Kano da Sebha : 66
4.1.5 Kamancin Kayayyakin yin Kaciya a Kano da Sebha : 69
4.1.6 Xakin yin Kaciya (Wurin yin Jinya) : : : 70

4.1.7 Abincin Xankaciya : : : : : 72
4.1.8 Lokutan Ziyara : : : : : : 73
4.1.9 Tufafin Kaciya : : : : : : 75
4.1.10 Gayyatar Kaciya : : : : : : 76
4.2 Bambance-Bambancen da ake Samu a Al'adun Kaciya a Tsakanin Hausawa Kanawa da Larabawan Sebha a Libya : : : : : : : 77
4.2.1 Kaciyar Sa-Wandonka : : : : : 77
4.2.2 Shekarun Kaciya : : : : : : 78
4.2.3 Ranar yin Kaciya : : : : : : 80
4.2.4 Kayayyakin yin Kaciya : : : : : 82
4.2.5 Maganin Kaciya : : : : : : 83
4.2.6 Bikin Kaciya : : : : : : 84
4.2.7 Wasu Al'adun Larabawan garin Sebha na Kaciya : 87
4.2.8 Wasu Al'adun Hausawa Kanawa na Kaciya : : 87
4.3 Bambancin Kayayyakin da Wanzaman Gargajiya a Garin Kano da Garin Sebha a Libya Suke Amfani da su a Wajen yin Kaciya : : : : : 87
4.3.1 Askar da Hausawa Kanawa Suke yin Kaciya da ita : 88
4.3.2 Almakashin da Wanzaman Sebha ke Amfani da shi Wajen Yin Kaciya : : : : : : 89
4.3.3 Karkiya Wadda Wanzaman Hausawa Kanawa Suke Amfani da ita a Wajen yin Kaciya a Gargajiyance : : : : : : 90
4.3.4 'Yarkara Wadda Wanzamai Hausawa Kanawa Suke Amfani da ita Wajen yin Kaciya a Gargajiyance : 90
4.3.5 Fatar Washin Askar yin Kaciya a Kano : : 91
4.3.6 Dutsen Washin Aska : : : : : 92

**BAI NA BIYAR**

**5.0 KAMMALAWA : : : : : : 94**

5.1 Tasirin Kaciyar Zamani a kan Al'adun Kaciya na Garin Kano a Nijeriya da Garin Sebha a Libiya : 94

5.1.1 Kaciyar Asibiti : : : : : : 98

5.1.2 Magungunan da Likitoci Suke Bayarwa Idan an yi Kaciya a Asibiti : : : : : 98

5.2 Abubuwan da Bincike ya Gano : : : : 99

5.3 Shawarwarin Bincike : : : : : 102

*Manazarta : : : : : : : : 105*

*Rataye na Xaya:*
*Hirarraki : : : : : : : : 107*

*Rataye na Biyu:*
*Kayayyakin da Wanzamai ke Amfani da su don yin Kaciya a Garin Kano : : : : : : 114*

*Rataye na uku:*
*Yadda Wanzamai Hausawa Kanawa Suke yin Kaciya : 117*

*Rataye na Huxu:*
*Hotunan Kayayyakin Abubuwa na Al'adun Kaciya a Garin Sebha na Qasar Libya : : : : 129*

*Rataye na Biyar:*
*Yadda Wanzami Yake Gudanar da Kaciya a Garin Sebha na Libya : : : : : : : 132*

## GODIYA

Ina godiya ga Allah subhanahu wa ta'ala wanda ya ba ni damar gudanar da wannan bincike cikin nasara. Sannan ina yabo da girmamawa ga Annabi Muhammad tsira da aminci su qara tabbata a gare shi.

Haka kuma ina gode wa jagoran wannan bincike Dr. Murtala Garba yakasai wanda ya duba wannan bincike ba tare da gajiyawa ba. Allah ya saka masa da alheri.

Sannan ina godiya ga Farfesa Aliyu Mu'azu mai duba wannan bincike na cikin gida, wanda ya sake duba wannan aiki tun daga farko har qarshe. Allah ya biya masa buqatunsa na alheri a duniya da lahira, malam ina godiya sosai.

Sannan ina mai matuqar farin cikin miqa gaisuwata ga malamina kuma uba Farfesa Sa'idu Muhammad Gusau wanda ya yi ta ba ni shawarwari, ya kuma yi mini gyare-gyare, duk da ximbin hidimomin da suke gabansa. Allah ya saka masa da alheri ya tallafi zuriyarsa.

Har ila yau ina miqa gaisuwata ga shugaban sashen nazarin harsunan Nijeriya da ke Jami'ar Bayero ta Kano Farfesa Aliyu

Mu'azu da Farfesa Abdulqadir Xangambo da Farfesa Isa Mukhtar da Farfesa Ahmadu Bello Zariya da Dr. Ibrahim Garba Satatima da Farfesa Yakubu Magaji Azare da Dr. Aminu Lawal Auta da Dr. Muhammad Tahar Adamu da Dr. Halima Abdulqadir Xangambo da Dr. Ahmad Magaji da Dr. Umma Ado Abbas da Dr. Umma Aminu Inuwa da Dr. Maryam Mansur Yola da Dr. Anas Sa'idu Muhammad da Malam Muhammad Ammani da Malam Muhammad Sulaiman da sauran malamai da ma'aikatan wannan sashe mai albarka. Allah ya saka wa kowa da alheri.

Har ila yau ina godiya ga hukumomin Jami'ar Sebha wadda ta xauki nauyin karatuna na digiri na biyu a Jami'ar Bayero, Kano. Allah ya saka musu da alheri.

Sannan ina godiya ga malamaina na Jami'ar Sebha. musamman Dr. Qassim Bilal wanda ya taimake ni sosai wajen gudanar da wannan bincke, Allah ya saka masa da alheri. Har wa yau ina godiya ga sauran malamaina na Jami'ar Sebha ta Libya, Allah ya saka wa kowa da alheri.

Akwai abokan karatuna, musamman Sunusi Mai'unguwar Giginyu da Abubakar Janguxe da Muhammad Jahun da sauran

xaliban M.A. Hausa na shekarar 2014-2017 na Sashen Koyar da Harsunan Nijeirya, Jami'ar Bayero ta Kano, waxanda su ma nake yabawa a gare su, musamman a kan zaman karatu na 'yan'uwantaka da muka yi a tare da juna. Har ila yau ina godiya ga wanzaman da na yi hira da tattaunawa da su a Kano da kuma a Sebha, Libya. Allah ya saka musu da alheri.

Sannan ina godiya ga Nasir Hassan Haris wanda ya buga wannan aiki a na'urar kwamfuta. Allah ya biya masa buqatunsa na alheri.

Daga nan ina miqa godiya ta musamman ga Malam Kamilu Xahiru Gwammaja, Ma'aikaci a Babban xakin karatu (Laburare) na Jami'ar Bayero, Kano wanda ya taimake ni da wasu kundayen bincike da bugaggun littattafai da muqalu waxanda na yi bitarsu a wannan bincike nawa, Allah ya saka masa da alheri.

Ina godiya ga al'ummar Jihar Kano waxanda suka nuna mini karamci, na gode Allah ya saka wa kowa da alheri.

Sannan ina yi wa matata, Sulxana Abdallah, wadda ta yi haquri da ni sosai a lokacin gudanar da wannan bincike, ga kuma

addu’ar da ta yi ta mini tana qarfafa guiwa. Allah ya saka mata da alheri.

## SADAUKARWA

Ina sadaukar da wannan aiki ga mahaifina Alhaji Mahdi Jibirl da mahaifiyata Hajiya Maryam Hassan. Ina roqon Allah ya saka musu da gidan Aljanna.

## GABATARWA

Wannan bincike ne wanda aka gudanar a kan kwatanta al’adun kaciya a tsakanin al’ummomi biyu wato Hausawa Kanawa da Larabawan Sebha na Libya. A cikin binciken an kawo kamanci da bambancin al’adun da waxannan suke gudanarwa a yayin yi wa yara kaciya. Sannan binciken ya kawo kamanci da bambancin kayayyakin da suke amfani da su wajen gudnaar da kaciya tare da fayyace kamanci da bambancin yadda kowacce al’umma a cikinsu take yin duk wani sha’ani da ya shafi kaciya. Haka kuma bincike ya fito da tasirin da kaciyar zamananci ta likita ta yi a kan al’adun kaciya na waxannan al’ummomi waxanda aka gudanar da binciken a kansu, wato Hausawa kanawa da Larabawan Sebha a Libya.

Sannan an kasa wannan bincike zuwa babi-babi har guda biyar, a inda aka gabatar da kowane babi kamar haka:

A babi na xaya an kawo bayanan share fage waxanda suka haxa da dalilan bincike da manufar bincike da muradun bincike da tambayoyin bincike da iyakancewar bincike da kuma gudummawar bincike.

A babi na biyu an fara ne da kawo tarihin garin da Kanawa, sannan aka kawo tarihin garin Sebha na Libya duk a taqaice sannan

aka kawo ma’anar kaciya da asali da tarihin kaciya a a duniya da tarihin samuwar kaciya a wajen Hausawan Kano da tarihin samuwar kaciya a garin Sebha na Libya. Sannan an yi bitar ayyukan magabata waxanda suka haxa da kundayen bincike da bugaggun littattafai da muqalu da takardun ilimi, waxanda aka yi bitarsu kuma suka ba wa wannan bincike hasken gudanar da shi cikin nasara.

A babi na uku an kawo ra’in da aka yi amfani da shi wajen gudanar da wannan bincike tare da bayyana hanyoyin da aka bi wajen tattara bayanan da aka yi amfani da su wajen gudanar da wannan bincike.

Haka kuma, a babi na huxu an kawo kamancin abubuwa guda goma na al’adun kaciya a tsakanin Hausawa Kanawa da  mazauna garin Sebha. Sannan aka kawo abubuwa guda tara waxanda suka bambanta al’adun kaciya a tsakanin Hausawa Kanawa da mazauna garin Sebha.

Har ila yau a babi na biyar an kawo tasirin kaciyar zamani a kan al’adun kaciya na garin Kano da garin Sebha a Libya, a inda aka kawo bayanin yadda ake kaciyar zamani ta asibiti wadda likitoci suke yi, sannan aka kawo magungunan da likitoci suke bayarwa idan sun yi wa yaro kaciya.

Haka kuma an kawo bayanan abubuwan da binciken ya gano tare da kawo shawarwarin mai bincike. A qarshe an kawo sunayen waxanda aka yi hira da su a cikin wanzamai na garin Kano da Sebha da masana da manazarta na qasar Nijeriya da Libya da likitoci na garin Kano da Sebha da tsofaffi na garin Kano da Sebha. Sannan an kawo ratayen hotuna na kayayyakin yin kaciya a garin Kano da Sebha. Kana a qarshe an kawo yadda ake kaciya a garin Kano da Sebha a Libya a cikin hotuna dalla-dalla.

# ABSTRACT

*This thesis entitled "Comparative analysis of cultural traditions of circumcision between Hausawa Kanawa and Arab People of Sebha in Libya" the research traces the historical background of circumcision among Hausawa Kanawa and people of Sebha in Libya. The research attempt to account for the traditional activities, cultural ceremonies as well as the cultural method of circumcision between Hausawa Kanawa and people of Sebha in Libya. This research applied Edward's theory (1959) of comparative cultures to analyses the phenomenon largely on interview, books review, observations and critical research processes.*

## TSAKURE

*Wannan bincike ne da aka sa wa suna "Kwatancin Al'adun Kaciya a Kano (Nijeriya) da Sebha Libya". Binciken ya bayyana asalin tarihin kaciya a wajen Hausawa Kanawa da Larabawa mazauna garin Sebha a Libya. Haka kuma binciken ya bayyana al'adu da bukukuwa da yadda ake gudanar da kaciya a wajen Hausawa Kanawa da mazauna garinn Sebha na Libya. An yi amfani da ra'in Edward (shekarar 1959) domin nazarin kwatanta al'adu. Binciken ya mayar da hankali wajen gano al'adun da suka yi kamanci da waxanda suka bambanta a vangaren kaciya a tsakanin Hausawa Kanawa da Larabawa mazauna garin Sebha, ta hanyar tattaunawa da hira da yin bitar littattafai da ziyartar gani da ido da yin cikakken bincike.*

## BABI NA XAYA

## 6.0 SHARE FAGE

Wannan bincike ne da aka gudanar a kan al’adun kaciya na Hausawa Kanawa da Larabawan garin Sebha a Libya. A binciken an kawo bayanan al’adun kaciya na gargajiya waxanda Hausawa Kanawa suke gudanarwa ta fuskar bikin kaciya da tufafin kaciya da lokacin aiwatar da kaciya da sauran al’adun da ake aiwatarwa a dalilin yi wa yaro kaciya da al’adun kaciya na gargajiya waxanda Larabawa Larabawan garin Sebha suke gudanarwa, kuma al’ummarsu suka yadda wannan al’adu nasu ne sannan suka ci gaba da aiwatar da su a duk lokacin da za a yi wa yaro kaciya kamar kafa tuta da yi wa yaro carbin kuxi da sauran al’adun kaciya irin nasu. Sannan aka kawo kamancin al’adun da kuma bambancinsu a tsakanin waxannan al’ummomi waxanda aka gudanar da binciken a kansu wato Hausawa Kanawa da Larabawan Sebha na Libya ta hanyar bayanai da misalai.

Shi kuma wannan babi na xaya ya qunshi bayanai ne na share fage waxanda suka haxa da dalilan bincike da muradin bincike da tambayoyin bincike da iyakancewar bincike da kuma gudummawar da ake sa ran wannan bincike zai ci gaba da bayarwa.

## 6.1 Dalilan Bincike

Dalilan da suka sanya yin wannan bincike sun haxa da sha'awar raya al'adu da kiyaye su, musamman a irin wannan zamani na game-duniya. Saboda haka ake ganin xaukar al'adun kaciya a birnin Kano na qasar Hausa da al'adun kaciya na garin Sebha a qasar Libya a duba yadda ake gudanar da su da nufin adana su a wallafe cikin kundi xaya abu ne mai muhimmanci.

## 6.2 Manufar Wannan Bincike

Manufar wannan bincike ita ce nazartar al'adun kaciya a garin Kano na qasar Hausa da garin Sebha na qasar Libya domin a tantance al'adun kaciya waxanda suka ratsa al'ummar Hausawa a Kano da waxanda Larabawa na garin Sebha a Libya suke aiwatarwa a lokacin yi wa yara kaciya.

## 6.3 Muradun Bincike

Muradun wannan bincike sun qunshi:

i) Niyyar gwada yadda alaqar al'adun Hausawa Kanawa suke da al'adun Larabawan Sebha ta qasar Libya;

ii) Taskace al'adu waxanda Hausawa Kanawa da Larabawan Sebha suke aiwatarwa a lokacin yin kaciya musamman saboda barazanar da suke fuskanta daga zamananci;

iii) Gwada irin tasirin da zamananci ya yi wa al’adun kaciya a garin Kano na Nijeriya da garin Sebha a Libya.

## 6.4 Tambayoyin Bincike

Kowane bincike musamman ma na al’adun mutane mabambanta, akwai ire-iren tambayoyin da ake sa ran za a amsa idan binciken ya kammalu cikin nasara, wannan bincike ma ana sa ran zai amsa waxannan tambayoyin:

i) Yaya Hausawa mazauna Kano suke aiwatar da al’adun kaciya?
ii) Yaya Larabawan garin Sebha na qasar Libya suke aiwatar da al’adun kaciya?
iii) Su wane ne ake yi wa kaciya a Kano da Sebha?
iv) Waxanne kayayyaki ne ake amfani da su a kaciyar gargajiya a Kano da Sebha?
v) Mene ne tasirin kaciyar yara maza ga Hausawa a Kano da kuma Larabawan Sebha a Libiya?

## 6.5 Iyakancewar Bincike

Iyakar wannan bincike ita ce nazarin al’adun kaciya a tsakanin Hausawa mazauna birnin Kano da kuma Larabawa mazauna Sebha a Libya don fito da kamanci da bambance-bambancen da ake samu a lokacin da suke yi wa yaransu kaciya tare da fito da tasirin zamananci a kan al’adun waxannan al’ummomi na vangaren kaciya.

Sannan wannan bincike an aiwatar da shi ne tun daga watan Fabrairu, 2016 zuwa watan Fabrairu, 2018.

## 6.6 Gudummawar Bincike

Kowane bincike na ilimi idan an kammala shi akwai nau'o'in gudummawar da binciken zai ci gaba da bayarwa, wannan bincike da aka gudanar zai ci gaba da bayar da waxannan gudummawoyi kamar haka:

i) Zai zamo wani kundi guda xaya wanda aka taskace al'adun kaciya na Hausawa Kanawa da Larabawa na garin Sebha tare da fayyace kamanci da bambancin al'adun da waxannan al'ummomi Larabawan garin Sebha na Libya da Hausawa mazauna garin Kano na Nijeriya ta vangaren kaciya. Kuma zai zamo matattarar bayanai waxanda masu son yin bincike a kan kaciya za su amfanu da su.

ii) Zai daxa qulla zumunci a tsakanin Hausawa mazauna birnin Kano a Nijeriya da Larabawa Larabawan garin Sebha a qasar Libya.

A wannan babi an kawo bayanan share fage ne waxanda suka haxa da dalilan gudanar da wannan bincike da manufar wannan bincike da muradin binciken da tambayoyin da wannan bincike ya amsa da iyakancewar wannan bincike da kuma gudummawar da ake sa ran wannan bincike zai ci gaba da bayarwa a fagen nazari.

## BABI NA BIYU

## 7.0 BITAR AYYUKAN DA SUKA GABATA

A wannan babi, za a kawo bayanai ne a kan binciken masana da manazarta da xaliban ilimi na kundayen bincike da bugaggun littattafai da muqalu waxanda suke da alaqa da wannan nazari da aka gudanar domin samun nasararsa. Sannan da farko sai da aka fara da bayyana tarihin garin Kano na Nijeriya da garin Sebha na Libya.

### 7.1 Tarihin Kano da Kanawa a Taqaice

Hausawa, kamar yadda Adamu (1997:16) ya bayyana al'umma ne, da suke zaune a qasar Hausa a cikin yankin Afrika ta yamma, kuma su Hausawa mutane ne baqaqen fata ba farar fata ba, ko da yake akan samu 'yan farare jefi-jifi musamman in aka samu auratayya da wata qabila.

Qasar Kano tana daga yankin tsakiya na arewacin qasar Hausa. Daga gabas ta yi iyaka da qasashen Barno da Bauchi daga yamma ta yi iyaka da Katsina daga kudu ta yi iyaka da kudan Zariya, daga arewa ta yi iyaka da qasar Nijar (Dokaji, 1978:1).

Almajir (2009: 22) ya rawaito (Gusau 1988:54) ya bayyana cewa farfajiyar Kano tana daga cikin wurare masu yalwa ainun da

albarkar qasa, don haka, noma ya zama babbar sana’a a wurin, sai dai kuma ana samun qarfen tama da ake haqo shi daga gindin dutsen Dala da sauran duwatsun da suke zagaye da wurin, wanda ake amfani da shi wajen qere-qere. Wannan yanayi na wurin ya sa mutane daga wurare daban-daban sun yiwo qaura zuwa gare shi.

Haka kuma Almajir (2009:22) ya rawaito cewa (Adamu, 1999:27) ya bayyana cewa garin Gaya wanda yake da nisan kilomita 60 daga Kano ya taka muhimmiyar rawa wajen samuwar Kano, domin ta zamto mahaxa ko kadarko ta masu yiwo qaura, musamman daga gabacin sudan da Maghrib da kuma gabas ta tsakiya. Wannan ya haxa da mutanen gabacin Sudan da suka guje wa yaqi. Sannan kuma Gaya ta samar wa da Kano sunanta, wato sunan wani shugaban mutanen da suka zo Kano daga can domin neman tama, tun a wajen qarni na bakwai (7), wanda suke yin amfani da shi domin kayan noma. Kano maqeri ne daga wani gari wai shi Dahlak ya fito saboda qarancin zaman lafiya. shi wannan gari a qasashen gabas yake, wanda ya yau yana cikin Eritrea.

Hausawa mutane ne masu tsananin riqon al’adunsu na gargajiya, musamman wajen tufafi da abinci da al’amura tsakanin dangi da abokai da shugabanni da kuma al’umuran sana’a ko kasuwanci ko neman ilimi da sauransu.

Tun daga zuwan Turawa har yau, Hausawa suna cikin al’umomin da ba su saki tufafinsu na gargjaiya sun ari na baqi ba. Galibin adon namiji a Hausa ba ya wuce riga da wando, musamman fanjama, da takalmi faxe ko sau-ciki da hula qube, ko dankawara ko zita ko havarkada, in kuma saraki ne ko malami ko dattijo, yakan sa rawani. Adon mata kuwa zani ne da gyauton yafawa, ko gyale, da kallabi, da taguwa, da xan tofi ko mukuru da ’yan kunne, da dutsen wuya, watau tsakiya ko murjani da awarwaro. A da can suna sa xan hanci, amma yanzu wannan adon ya gushe (Adamu, 1997:16).

Adamu (1997: 16) ya bayyana cewa: “Yawancin abincin Bahaushe kuwa ana yin sa ne da gero ko dawa ko maiwa, sai kuma sauran abubuwan haxawa, kamar su gishiri da garkono da daddawa da albasa da kuka da kuvewa da turgunnuwa da karkashi da lalo da tafasa da xata. Sai kuma kaya irin na marmari, kamar su wake da shinkafa da acca da Ibro da kuma kayan rafi da sauran makamantansu.

Yawacin Hausawa Musulmi ne, saboda haka mafi yawan al’adunsu da suka shafi aure da haihuwa da mutuwa duk sun dogara ne ga wanda addini ya nuna, sai xan abin da ba a rasa ba na daga al’adun gargajiya, musamman a wajen Maguzawa. Haka kuma

wajen mu'amala da iyaye ko dangi ko aboki ko shugabanni ko maqota ko wanin waxannan, yawanci na Musulunci ne. Haka kuma sana'a da kasuwanci da neman ilimi duk a jikin Musulunci suka rataya. Maguzanci kuwa addini ne ga gargajiya ba harshe ba ne, don haka ne ma masu cewa Hausawa Maguzawa ne suke kuskure idan suna nufin qabila ko harshe, idan kuwa suna nufin addinin Maguzanci to wannan daidai ne (Adamu, 1997:16-17).

A wajen Bahaushe can ainihi sana'a da harkar kasuwanci da harkar karatu suna bin gado ne, wato kowa yana bin yadda ya gada kaka da kakanni. Kuma idan mai sana'a ya shiga baqon gari, zai je ya sauka a gidan abokan sana'arsa ne. In ma koyo ya zo yi, zai je gidan masu sana'ar gidansu ne. Saboda haka kusan kowace sana'a akwai sarkinta da makaxanta da mawaqanta kai har ma da wasu al'adu na masu yin ta da suka sha bamban da na sauran jama'a (Adamu, 1997:17).

Misali: Ko a yanzu a qasar Hausa Sarkin makaxa da Sarkin wanzamai da Sarkin Fawa duk suna bin gado ne. A garin Safana na Jihar Katsina an naxa Dakta Bashir Sallau Safana a matsayin Sarkin Aska (Sarkin wanzamai) saboda wanzanci gadon gidansu ne, a she har yanzu a qasar Hausa sarauta ta sana'ar gargajiya tana bin gado ne.

## 7.2 Taqaitaccen Tarihin Garin Sebha a Libya

Idan ana magana game da birnin Sebha za mu iya cewa birnin yana cikin Afrika ta arewa a qasar Libya. Sebha ta rarrabu zuwa shiyya uku kafin ta faxaxu ta zama babban birni a yankin kudancin Libya, in aka duba taswirar Libya za a sami birnin Sebha a tsakanin layi (27-1) zuwa (27-7) gabas a faxin qasar Libya a ma'anunin (girintish), Haka kuma za a tarar tayi iyaka da hamadar sahara a gabacin qasar Libya, sannan a vangaren arewa ta iyaka da Al'shaxi, ta kudu masu yamma kuma ta yi iyaka da ubari da garin Gihart.

Al'ummomin da suke zaune a garin Sebha guda biyu ne, wato Larabawa da kuma Buzaye, a vangaren Larabawa akwai qabilu kamar haka: Aulad Sahal da Al-mahamid da Aulad Silaman da Al-qadadifa da Al-maqariha da Warfalla da Al-ansar da Al-hasawna da Al-zayadin da Al-ujala da Aulad busif da Aulad hidiri da Aulad-Wafi da Al-Fwayda da kuma Sahaka (Nash-Nash, 2009:27-28).

Al'umma ta biyu da take zaune a birnin Sebha su ne Buzaye, kuma a halin yanzu, a wata qididdiga da aka yi yawan mutanen da suke zaune a garin Sebha na Libya a shekarar 2009 an bayyana cewa mutanen da suke zauna a garin sun kai kimanin mutum dubu

xari uku da talatin da uku (333) (Nash-nash, 2009:32). Birnin Sebha birni ne wanda yake kewaye da gonaki ta kowane vangare, wannan ne ya sa birnin Sebha ya dogara da noma.

Abubuwan da ake nomawa a Sebha sun haxa da: Alkama da wake da masara da dabino da kankana da ciyawar da dabbobi suke ci da sauransu. Haka kuma za mu iya cewa birni ne wanda ya shahara wajen kasuwanci a cikin qasar Libya da ma wajen qasar, kamar su qasar Chadi da Nijar da Sudan, saboda su waxannan qasashe duk sun yi iyaka ne da qasar ta Libya.

### 7.3 Ma'anar Kaciya

Qamusun Hausa na Jami'ar Bayero (2006:222) ya bayyana ma'anar kaciya kamar haka:

> "Yanke lovar azzakarin yaro, yawanci idan ya kai shekara bakwai".

Shi ko Sallau (2009:87) ya bayyana ma'anar kaciya a gargajiyance kamar haka:

"Kaciya tana nufin yanke ko cire fatar da ta rufe kan azzakarin mutum. A qasar Hausa wanzamai ne suke yin kaciya, kuma mafi yawanci an fi yin kaciya a lokacin sanyi".

Kaciya al’ada ce wadda addini ya amince da ita, kusan dukkanin qasashen da suke bin tafarkin addinin Musulunci suna gabatar da kaciya ga ’ya’ya maza. Haka kuma wasu qasashen da ba Musulumi ba su ma suna yin kaciya. A wasu al’ummomi na duniya akan sami masu yi wa mata ma kaciya.

Sallau (2009:87-88) ya yi qarin haske a kan kaciya, ga abin da yace: “Dalilin da ya sa aka fi yin kaciya a lokacin sanyi shi ne, a wannan lokaci jikin mutum ya fi saurin tohuwa, don a wannan lokaci ko rauni mutum ya yi zai yi saurin warkewa. A lokacin sanyi kuma an kai ga amfanin gona, abinci ya wadata, yaran da aka yi wa kaciya za su sami wadataccen abincin da za su ci, jikinsu ya tohu da sauri su yi saurin warkewa, kuma a wannan lokaci aiki ya yi sauqi za a sami wanda zai tsaya ya riqa kula da su.

A al’adar Hausawa yawanci sai yaro ya kai shekara bakwai ko abin da ya yi sama da haka sannan za a yi masa kaciya. Hausawa ba su fiye yi wa yaro kaciya yana da shekara takwas da haihuwa ba. Saboda an camfa wai idan aka yi wa yaro kaciya yawan da shekara takwas, to wani bala’i na iya faxa masa. Wannan ne ya sa idan ba a yi wa yaro kaciya yana da shekara bakwai ba, to ba za a yi masa ba, sai ya kai shekara tara ko goma. A da idan za a yi kaciya ana tara

yaran unguwa xaya a gida xaya domin yi masu kaciya, a sanya mutum xaya ya tsare su yana kula da su don kar su fama kaciyar. Amma a yanzu wasu suna yin haka, wasu kuwa da sun tashi yi wa ’ya’yansu kaciya, sai su kira wanzami ya yi kaciyar ba tare da sun gaya wa kowa ba (Sallau, 2009:87).

Shi kuma Moza (1993:183) a cikin littafinsa (*Susoligyi Abadat wal taqalid li marhala milad til mushtoma’a al’imarat)* cewa ya yi: shayi (kaciya) a musulunci ana yinta ne saboda tsabta, sannan a kuma cire fatar azzakari ta namiji mara amfani. Haka kuma wannan al’ada ana samun ta a cikin wasu qasashen Larabawa, a wajen mata da maza, ana gudanar da wannan biki a cikin jama’a kamar ’yan’uwa da maqwabta da abokan arziki. Ana shirya musu gagarumar walima, wani lokacin takan zama kamar na bikin kaciya. Wannan biki na kaciya ana yinsa har tsawon mako guda. Kuma waxanda su ke hallara bikin sukan bayar da tsaraba domin a ba wa yaro ko yaran da aka yi wa kaciya. Sannan a al’adance an fi yin kaciya a ranakun Juma’a ko Litinin, soboda raya sunnar Annabi Muhammadu, sallallahu alaihi wa sallama”.

Al-Samarra’i (2004:180) kuwa cewa ya yi “Kaciya sunna ce ta addinin Musulunci, kuma tana daga cikin tsafta da kariya daga

wasu cututtuka, sannan kuma tana xaya daga cikin al’adun Musulunci. Musulmi ya fi son ya yi kaciya a cikin jama’a wato, yaro a yi masa shayi (kaciya) tare da ’yan’uwansa da yaran maqwabta, haka kuma ya ci gaba da cewa an fi yi wa yaro kaciya tun yana jariri, sannan ana yi ne a cikin farin ciki da shirye-shiryen walima tare da jama’a”.

## 7.4 Asali da Tarihin Kaciya a Duniya

Sallau (2013: 153) ya bayyana cewa a al’adar Hausawa sai yaro ya kai shekara bakwai ko fiye da haka ne za a iya yi masa kaciya, amma ba a yi wa yaro kaciya yana da shekara takwas da haihuwa, dalili shi ne an camfa, don kuwa an xauke yin kaciya ga yaro mai shekara takwas da haihuwa zai iya haifar masa da wani bala’i, wannan dalili ne ya sa idan ba a yi wa yaro kaciya a lokacin da yake da shekara bakwai ba, to ba za a yi masa ba sai ya kai shekara tara ko ya wuce tara da haihuwa. A lokacin da za a yi kaciya iyayen yara na unguwa xaya ko haxo kan yara waje xaya don ayi musu kaciya, kuma ana tsayar da mutum wanda aka tabbatar yaran na tsoron sa da yar riqa kula da su har sai sun warke.

Haka kuma sallau (2013:154) ya rawaito abin da Abil-Azahiri ya bayyana a game da al’adun kaciya bayan samuwar addinin musulunci. Ga abin da yace:

> “Addinin Musulunci ya yi tasiri na azo a gani a kan al’adun kaciya a qasar Hausa. Da farko dai shari’a ta bayyana yin kaciya ga maza sunna ce mai qarfi. Ana yin kaciya domin qarin tsabtace jiki a lokacin wankan janaba ga wanda ya sadu da iyalinsa. Abin nufi a nan shi ne. wanda ba a yi wa kaciya ba idan ya sadu da iyalinsa zai fuskanci matsalar wanke dukkan dattin maniyyin da ya taru a kan azzakarinsa saboda fatar ta tattare ta rufe kan azzakarin, shi kuwa wanda aka yi wa kaciya saboda an yanke wannan fata, ba zai fuskani wata matsala a lokacin da ya zo wanke ta ba. Ga su matan, sun fi jin daxin saduwa da mazajen da aka yi wa kaciya. Wannan ya qara taimaka wa Hausawa su riqa yi wa ’ya’yansu kaciya don bin shari’ar addinin Musulunci”.

Haka kuma Sallau (2013: 154-156) ya ruwaito Kwairanga (2000) ya bayyana asali da al’adun kaciya, domin cewa ya yi “Ta fuskar lokacin da ya dace a yi wa yaro kaciya shari’ar addinin Musulunci ta bayyana, sai yaro ya kai shekara bakwai zuwa shekara goma da haihuwa za a yi masa kaciya, amma kuma kar a bar su su kai shekarun balaga ba a yi musu ba. wato bidi’a ce a fannin kaciya a jinkirta yi wa mutum kaciya har sai ya balaga; yin haka bidi’a ce haramtacciya a bisa gamuwar malamai, domin kuwa yin haka koyi ne da maguzawa. Haka kuma yana daga abin qi, yi wa jariri kaciya a rana ta bakwai da haihuwa don kuwa

yin haka ko yi ne da Yahuduwa. Wannan ma ya qara taimaka wa Hausawa su riqa yi wa ’ya’yansu kaciya suna da shekaru bakwai da haihuwa.

A wani bincike da aka gudanar an fahimci dalilin da ya sa shari’a ta tsara yi wa yara kaciya cikin waxannan shekaru. A sakamakon binciken an gano cewa ire-iren yaran da aka yi wa kaciya suna jarirai ba su fiye qarfin azzakari ba idan suka girma. Ire-irensu a lokacin da su ka yi aure matansu ba su fiye jin daxin jima’i kamar yadda za su ji daxi ga wanda suka shekara bakwai zuwa goma da haihuwa kafin a yi musu kaciya ba. dalilin da ya kawo haka shi ne ba a bar azzakarin yaci abincinsa ba, wannan fata fara ta cikin wadda ta lulluve kan azzakari wato lova. Idan aka bar azzakari ya ci abincinsa ya qoshi, zai yi kauri da juriya idan aka zo yin jima’i. An bayyana cewa bidi’a ce a fannin kaciya a jinkirta yi wa yaron da suka isa yin kaciya, har sai wasu qannensu sun isa don ayi masu tare, yin haka bidi’a ce haramtacciya idan jiran ya kai har waxanda za a yi wa kaciyar suka balaga.

Idan kuwa jiran bai kai haka ba, to bidi’ar makaruhiya ce wani bayanin kuma ya nuna, bai kamata a hana yara yin kuka a lokacin da za a yi musu kaciya ba, a saboda haka tsorota yara don

kar su yi kuka a lokacin da za a yi masu kaciya bidi'a ce haramtacciya bisa gamuwar malamai.

Haka kuma ya zo a cikin risalar xan Yusif xan Salim xan Ibrahim, inda aka bayyana cewa "Nishin marar lafiya ma tasbihi ne, yin qararsa kuwa hailala ce, numfahsinsa kuwa sadaka ce, barcinsa ibada ce, jujjuyawarsa daga wannan kuvi zuwa wancan kamar jihadi ne don xaukaka kalmar Allah, kuma za a ci gaba da rubuta masa lada fiye da yadda ya ke yin ibada alokacin da yake da lafiya". Saboda haka, kamata ya yi abar yara su yi kukansu idan an zo yi musu kaciya, don yin kukan zai sa a rubuta musu lada mai yawa, su kuma waxanda suke tsoratar da yaran suna zare masu idanu, su ce; idan suka ji tsoro za su dake su, ko za su kashe su, da dai sauran tsoratar", wato ire-iren waxannan mutane suna daga cikin shaixanun mutane vatattu. Kuma duk wanda ya aibata yaran ko ya zarge su don kukan da suke yi a lokacin da aka yi musu kaciya, to yana da laifi, ya wajaba a gare shi ya tuba, ya nemi gafara wajen Allah.

### 7.4.1 Tarihin Kaciya a Wajen Hausawan Kano

Sallau (2013:153) ya bayyana cewa kaciya na nufin yanke ko cire fatar da ta rufe kan azzakarin mutum. A qasar Hausa wanzamai

ne suke yin kaciya, kuma an fi yin kaciya a lokacin sanyi. Dalilin yin ta a wannan lokaci shi ne, Hausawa sun xauka tafi saurin warkewa, kuma a wannan lokaci an kai ga amfanin gona abinci ya wadata. Wannan ne zai qara taimaka wa yaron da aka yi wa kaciya ya sami wadataccen abinci mai gina jiki yadda zi yi saurin warkewa. Kuma a wannan lokaci ayyukan sun fara yin sauqi, za a sami wanda zai tsaya, ya kula da sun yi wani mugun wasa wanda zai sa su yi fami a kaciyar da aka yi musu ba.

Haka kuma sallau (2010:103-104) ya ci gaba da cewa a al'adar Hausawa idan za a yi wa yara kaciya iyayan yaran na aika wa danginsu da abokan arzikinsu na kusa da na nesa, su sanar da su cewa za a yi wa wane kaciya a ranar kaza. Idan ranar ta zo dukkan dangi na kusa da na nesa da abokan arziki sai su taru a gidan domin bakin kaciyar. Iyayen yaron za su yi abinci, a kuma daka gero a yi garin da za ayi kunun kanwa wanda za a ba yaran da aka yi wa kaciyar, bayan gama kaciyar sai maroqi, wani lokacin ma har da makaxa za su sanar da mutanen da suka taru a wurin kaciyar cewar yaron ya girma. Daga cikin ire-iren kalaman da ke fitowa bakin maroqan na nuna an gama kaciya sun haxa da:

“A kawo kari yaro ya girma”
“ A kawo karin kugunu”
“A kawo karin ba saukon daka”
“A Kawo karin gama faxa, sa faxa”
“A kawo karin ta wando”
“A kawo karin a bin ginar jarirai”

Daga nan ne sai dangi da abokan arziki su yi ta yi wa wanzamin da ya yi kaciyar da kuma yaron da aka yi wa kaciyar kyauta. Akan samu wasu yaran abubuwan da dangi suka tattara masu a lokacin da aka yi musu kaciya su zama dalilin arzikinsu. Domin kuwa wasu dangi da abokan arziki kan ba yaron da aka yi wa kaciya dabbobi waxanda sunnu a hankali sai su yi ta yaxuwa har su yi yawa.

Shi kuma Durumin’iya(2006:57-59) cewa ya yi kumar yadda Bahaushiyar al’ada ta tanada ana yi wa yara maza kaciya ne yayin da suka kai kimanin shekaru shida ko bakwai da haihuwa. Mafi yawancin lokuta akan tattara yara ne sa’annin juna a yi musu kaciya lokaci guda. Ko dai ’ya’yan ’yan’uwa ko kuma abokai ko kuma na maqwabta. A da, gabanin zuwan addinin musulunci qasar Hausa, tarihi ya nuna cewa akwai savanin zamantakewa da tafarkin rayuwa a tsakanin Hausawa na wancan lokaci. A wasu gundumomin ma ba a yin kaciya kwata-kwata. Misali a qasar Kano an samu wasu

gundumomi kamar qasar Rano da Gwarzo da Tudun Wada. Mazauna waxannan gundumomi ba su yin kaciya a wancen zamani. Haka kuma an samu a qasashen Zazzau da Zamfara da Katsina da Daura da sauran sassan qasar Hausa, wasu suna yi amma fa ba kowane lokaci ba, wasu kuma sai mutum ya girma ya kai munzalin aure, sannan ake yi masa kaciya. Ala kulli halin an haqiqance da cewa kaciya ko kuma tuje ko yanke lova ga xa namiji a qasar Hausa ya samu gindin zama ne da qarvuwa hannu biybbiyu bayan da addinin musulunci ya zo ya kuma kafu.

Bahaushiyar al’ada ta tanadi ranar juma’a ta yanayi na hunturu ko sanyi ta zamanto ranar da kuma lokacin da ake yin kaciya. Babu wani nafsi da ya zo da cewa dole sai a wannan rana ne za a iya yin kaciya, wataqila, Hausawa suna yin kaciya ne ranar Juma’a domin girmama ta da kuma darajar da ranar take da shi a idanun musulmin duniya. Amma dai mafi yawanci an fi yin kaciya ranar juma’a da hantsi. A wannan rana, ana tuqa tuwon shinkafa miyar taushe. Haka kuma ’yan’uwa mata sukan taru a gidan da za a yi wa yaran ko kuma yaro kaciya. Da sassafe, za a yi wa xan kaciya wanka. Sannan a zo a zaunar da shi a tsakar gida ko kuma shamaki ko soro wanda a nan ne za a yi kaciyar.

Daga nan za a tanadi rami mai xan zurfi, a zaunar da yaran, a tattale qafafuwansa, sanann zakarinsa yana bakin ramin da aka haqa. Daga nan za a sami wani mutum mai qarfi ya riqe yaron ta baya, sannan a rufe masa ido, daga nan sai wanzami ya zauna a gaban yaran, ya kama zakarin yaron ya murza fatar lovar yaron (bayan saman zakarin). Daga nan sai ya xauko wani garin magani ya barbaxa ya ci gaba da murzawa da durzawa har sai ya fitar da wani darva-darva fari da yake daskarewa a kan zakarin yaron. Daga nan sai ya xauko wani xan kara ko tsinke ya auna zakarin ya kuma daidaita fatar.

Daga nan sai ya xauko askar kaciya wato ’yar kaciya ke nan, sai ya yanke. Da zarar ya yanke sai mata su rangaxa guxa. Daga nan sai wanzamin ya xauko ruwa da aka sa kanwa ko alumun a ciki ya kwara a kan kaciyar, sai kuma ya xauko wani garin magani na dakakkiyar qirya ya barbaxa. Daga nan an gama kaciya. Wanzamin zai buxe jakarsa ya xauko matashi (wato wasu ’yan karare ne waxanda tsawansu bai fi tsawon xan quri ba da yake xauke da zaren abawa, sai a zura zakarin xan kaciya a ciki kararan sai su zauna tsakanin zakarin da kuma marainan xan kaciya, sai kuma ya xauro shi ta qugun ko kwankwasan yaron, ya kuma qulle shi. Daga nan sai

wanzami ya xauko karkiya yace: “idan yaron zai kwanta barci sai a xaura masa domin ka da ya haxe qafafuwansa.

Daga nan sai ya xauko magungunan gargajiya ya bayar, ya ce “a dinga sa wa xan kaciya a abinci ko ruwa ko koko. Daga nan sai a tashi xan kaciya zuwa xakin da zai yi jiyya. ’Yan’uwa mata da abokan wasa sai a yi ta zuwa ana duba xankaciya, ana kuma xan tsokanarsa. Al’ada ta tanadar wa xankaciya zama wuri guda. Sannan abincin xankaciya ya haxa da cin naman kaji da shan zuma da kuma shan magungunan da wanzami ya bayar. Wanzamin ana sa vangaren zai riqa zuwa yana duba xankaciyar bayan kwana uku-uku ko sati-sati, domin ganan ci gaban kaciya a qasar Hausa.

Bugu da qari kuma, duk sauran nau’o’in ayyuka da wanzami yake yi a Bahaushiyar al’ada, kamar gyaran fuska ko aski ko sakiya ko saran kofaton dabbobi, akwai nasu irin nau’o’in kayan aiki da kuma irin yadda za a gudanar da shi.

Hausawa suna da sunaye waxanda suke kiran kaciya kamar haka:

- Kaciya
- Silli
- Kuido
- Shayi
- Sha

Sannan Hausawa kafin zuwan Musulunci wasu daga cikinsu suna yi wa mata kaciya saboda wasu dalilai kamar yadda Rakiya Adamu ta rawaito cewa: "Jaridar *Aminiya*, ta tattauna da Muhammadu Sagir Wanzan, wanda ake yi wa laqabi da Sagir xansanda da ke sana'ar wanzanci a Jihar Legas ranar juma'a, 25 ga watan Janairu shekarar 2015, ya bayyana cewa "Kaciya tana qara wa mata lafiya da kuma samun qwarin gwiwar saduwa da xa namiji. Idan kuwa ba a yi wa mace kaciya ba har angurya ta fito mata babu shakka za ta sami matsala" (Rakiya 2015).

Haka kuma Hausawa kwata-kwata ba su karvi wannan al'ada ta yi wa mata kaciya ba, musamman a wannan lokaci da ilimi ya wadata a cikin Hausawa, kamar yadda Rakiya Adamu ta rawaito cewa: "Malam Isa Wanzami mazaunin Dukawuya ya tabbatar mata Hausawa ba su karvi wannan al'ada ta yi wa mata kaciya ba" sannan ta rawaito cewa Dr. Sallau Safana na Jami'ar Umaru Musa 'Yar'aduwa ya tabbatar mata cewa: "Al'adar yi wa mata kaciya Bahaushe bai karve ta ba kwata-kwata, kuma ba ta cikin tsarin rayuwarsa (Rakiya 2015).

### 7.4.2 Tarihin Kaciya a Wajen Larabawa Larabawan garin Sebha

Al'adun kaciya wani gagarimin biki ne wanda ake yinsa a qasar Libya. Biki ne wanda ake xaukar kwanaki ana gudanar da shi, saboda muhimmancinsa a wajen al'ummar qasar Libya, ana yin waqe-waqe da kaxe-kaxe da kuma raye-raye a yayin gudanar da bikin na kaciya, kafin ranar kaciya mutanen gida (mahaifan yaron da za a yi wa kaciya) suna haxuwa a tsakar gida su shimfixa tabarma a zuba kayan qamshi irin su turare da lalle da kanunfari sai a sa su a cikin kwanon shan ruwa a kwava su tare, daga nan sai a kawo farin yadi a yanka shi qanana-qanana a zuba wannan abubuwa da aka qwaba a cikin waxannan guntattakin yadukan, sai a xaxxaure su. Idan ranar kaciya ta zo sai a rarraba wa mutanen da suka zo bikin na kaciya, ana yin xauri kamar talatin ko arba'in, a ranar kaciya mahaifiyar yaron da za a yi wa kaciya takan yi wa yaron addu'a a inda za a sa masa hula wadda take xauke da qahonni guda biyar qanana waxanda ake kira da "حويثه" "خميسه" "قرين" wato "kifi" da "biyar" da "qaho" (Hira da A'isha Abdulsalam).

Daga nan sai a rufa wa yaron riga sai 'yan'uwansa mata su kawo turare su sa a wajen, sannan a kawo yadi fari da kwano da qwarya, ana rufe kwanon da farin yadi, sai a kawo yashi a tanqaxe shi a zuba a cikin kwanon a rufe da farin yadi. Daga nan sai

mahaifin yaro da ’yan’uwansa su zo su biya masa kuxin kaciya a wajen wanzami, sai a zauna da yaron a kan qwarya ko kwanon da aka rufe da farin yadi, sannan a riqe shi wanzami ya yi masa kaciya. Ana gama yi masa kaciya sai mata su rangaxa guxa da waqa, ga waqar kamar haka:

سيدنامحمد والشيطان غاب       فرشنا الحصيره وغربلنا التراب
طهريامطهر صح الله ايديك       ولا توجع الغا لى ولاتغضب عليه

Saboda Annabi Muhammadu shaixan ya bar nan wajen,
A sa tabarma a tanqaxe qasar nan.

Wanzami ka yi kaciya Allah ya sa hannunka ya yi kyau,
Ka yi a hankali kar ka yi fushi da shi.

A lokacin da za a fara kaciya za a kawo kwano cike da ruwa sai uwar yaro ta sa qafarta a ciki, ba za ta cire ba sai an gama yi wa xan nata kaciya, daga nan sai a kawo hular yaron a ajiye sai mutane su rinqa bayar da gudummawa suna sa wa a ciki musamman kuxi ko dabbobi ko kayan abinci ko kuma sutura, sannan a rufa wa yaro tufafinsa na bikin kaciya. Kuma kuxaxen da aka tara su ne ake yi wa yaro carbin kuxi da su a rataya masa a wuya a lokacin da aka yi masa kaciya[1].

---

[1] Hira da Amina Ali Muhammad ranar 22/2/2016 a garin Sebha dake qasar Libya.

A al’adance idan za a yi wa yaro kaciya mahaifin yaro zai je ya sami wanzami ya sanar masa cewa zai kawo xansa a yi masa kaciya. Ana so wanzami ya zamo babban mutum kuma malami wanda ya haura shekara arba’in, sannan ya kasance mutum mai ladabi da biyayya sannan ya zama mahaddacin *Al’qur’ani* kuma a ya zamo malamin zaure wanzamin yana sa kamar tsawan sati xaya a matsayin ranar kaciya, sannan a al’adar mutanen garin Sebha an fi yin kaciya ranar Talata ko Laraba, a cikin satin da wanzami ya bayar mata sukan yi hidomin tare da maqwabta da ’yan’uwan yaron da za a yi wa kaciya, akan shirya kayan abinci iri-iri, sannan a xinka wa yaron rigar da zai sa a ranar da za a yi masa kaciya, a ranar mutanen da aka gayyata za su zo suna raye-raye da kaxe-kaxe da waqe-waqe da ganguna (Hira da Isa Muhamamd Mabrok).

Wanzami zai zo da jakunkuna guda biyu, xaya tana xauke da kayan aikin kaciya xaya kuma tana xauke da *Alqur’ani* mai girma izu sittin a cikinta, za a shirya yaron da za a yi wa kaciya a sa masa kaya sababbi, sannan a rufa masa wani bargo wanda ake kira da (جرد) da Larabci, sannan za a sa wa yaron hula sabuwa. Wanzami zai zo wurin da aka ware za a yi wa yaron kaciya tun safe, idan an gama kaciya mata za su yi guxa, sannan za su ci

gaba da kixe-kixe da waqe-waqe, kowa zai ta murna da farinciki, daga nan sai ’yan’uwa da abokan arziki da maqwabta su shiga bayar da gudummawa ga iyayen yaron da aka yi wa kaciya, wasu sukan bayar da akuya wasu kuma sukan bayar da kaji wasu kuma sukan bayar da kuxi ne, ana shirya xaki na musamman wanda yaron da aka yi wa kaciyar zai zauna a cikinsa ya yi jinya. Sannan ana ware ranar biyan wanzami haqqinsa, a wannan rana ’yan’uwan yaron da aka yi wa kaciya sukan taru amma anfi kirawo tsofaffi mata, za a haqa qaramin rami a sa itace a ciki a qona shi har sai ya zama toka sai a kamo xan kaciya a ajiye shi a bakin ramin, sai a shafa masa tokar itacen da garin magani wanda wanzami ya bayar a kaciyarsa, sannan a qyale shi har tsawon mintina kamar goma zuwa ashirin sai a ciro yaron a tafi da shi gida ana kaxe-kaxe da waqe-waqe ana guxa ana murna[2].

### 7.5 Bitar Ayyukan da Suka Gabata

A nan kuma za a yi bitar ayyukan da suka gabaci wannan nazari ne domin a sami bayanan da za su qara ba da haske a wannan bincike.

[2] Hira da Isa Muhammad, xan shekara sittin da biyar (65) mazaunin garin Sebha na qasar Libya.

### 7.5.1 Kundayen Bincike

Kundayen bincike su ne binciken da manazarta neman ilimi ko xaliban ilimi suka gudanar domin samun wani matsayi na karatu. Daga cikin kundayen da aka yi bita akwai:

Ibrahim (1982) ya gabatar da bincike a digirinsa na biyu mai suna "Dangantakar Al'ada da Addini: Tasirin Musulunci kan rayuwar Hausawa ta Gargajiya". A cikin bincikensa ya yi bayanin yadda wanzamai suke yin kaciya a qasar Hausa, a inda ya ce: "Ana yi wa yara kaciya a qasar Hausa daga shekara biyar izuwa tara (5-9), sannan ana tara yara da yawa a kira wanzami ya yi musu kaciya kuma ana haqa rami inda jini zai zuba, sannan a xakko yaro a rufe masa idanuwa a yi masa kaciya, wasu kuma yaran da sun zo kallo sai a yi musu kaciya sai dai a sanar da iyayensu cewa an yi musu kaciya. Sannan ya kawo al'adun da Hausawa suke yi a yayin da suka yi wa yaransu kaciya, haka kuma ya kawo yadda wanzamai suke bayar da magani har kaciya ta warke".

Wannan bincike ya daxa fayyace min komai na yadda Hausawa suke yin kaciya a gargajiyance, kuma na fahimci al'adun da Hausawa suke yi da zarar sun yi wa 'ya'yansu kaciya a gargajiyance, saboda haka wannan bincike ya taimaka wa wannan nazarin da nake gudanar wa da bayanai masu inganci.

Gixaxo (1988) ya gabatar da kundin bincike a kan “Asali da al’adun Miyawa”. A cikin bincikensa ya kawo bayanai a kan musulman qabilar Miyawa tare da bayyana yadda suke yi wa yaransu kaciya a ranar suna, kuma wasu daga cikin qabilar Miyawa sukan yi wa yaransu kaciya daga shekara biyu zuwa shida (2-6).

Sannan sukan tara yaransu su yi musu kaciya daga shekara zuwa shekara, idan ba a yi wa yaro kaciya a wannan rana ba, to sai wata shekarar. Wato kowace shekara sukan tara yara a guri xaya kuma a rana xaya su yi musu kaciya, sannan ba sa kiran wanzami ko su kai yaransu asibiti, wato duk shekara sukan gina xakuna a kurmin dodanni da ke bisa manyan duwatsu dake tsakiyar gari, a inda za a shigar da yara ana yi musu kaciya.

Wannan bincike, ya daxa ba ni haske a kan yadda matsayin kaciya take a al’adun sauran al’ummomin duniya, waxanda suke yin wasu abubuwa masu ban mamaki a dalilin yi wa yaransu kaciya.

Tanko (2000) ya yi bincike a kundin digirinsa na biyu mai suna “Tasirin Harshe da Al’adun Hausawa a kan Gwarawa” aikin bincikensa ya kawo al’adun kaciya ta vangaren wanzamai da ’yan’uwan yaran da aka yi wa kaciya a cikin al’ummar Hausawa da Gwarawa, a inda ya bayyana cewa Hausawa sukan yi bikin kaciya

kafin xankaciya ya warke, amma su Gwarawa duk da wannan biki na kaciya ya yi tasiri a cikinsu, sai dai su suna yin bikin kaciya ne bayan yaro ya warke gaba-xaya, sannan ya yi bayanin kayayyakin wanzanci a wajen Hausawa da Gwarawa, ya yi bayanin yadda Hausawa da Gwarawa suke yin kaciya.

Wannan bincike ya taimakeni sosai wajen sanin yadda Hausawa suke yin kaciya, sannan na daxa gane kayan aikin kaciya a qarsar Hausa, sannan na fahimci al'adun da Hausawa suke yi idan an yi wa yaro kaciya, wannan bincike ya taimakeni sosai a wannan Nazari da nake gudanarwa.

Sallau (2000) ya gabatar da kundin bincike na samun digiri na biyu, "Wanzanci: Matsayinsa na al'ada da sana'a a qasar Hausa", a wannan kundin nasa ya yi bayanin kamar haka:

Ya kawo bayanin kaciya da matsayin addinin musulunci a kan kaciya da matsayin likitoci a kan yadda wanzamai ke yin kaciya, ya kawo yadda wanzamai ke yin kaciya, ya kawo yadda ake bikin kaciya a qasar Hausa, sannan ya kawo abubuwan da ake amfani da su a wajen kaciya, kamar yankara da karkiya da guna da turvuwa mai sanyi da sauransu, sannan ya yi bayanin yadda ake yin kaciyar sa wando.

Haka kuma Sallau (2000) ya xauki kayayyakin al’adun kaciyar ta Hausawa xaya-bayan-xaya ya yi bayaninsu. Misali: ya bayyana yankara da cewa wani sullan karan dawa ne da ake yankawa guntu-guntu kamar tsawon rabin qaramin yatsa na babban mutum. Su ‘yankara ana samun guntaye uku ne sai a rarake kowane a yi masa qofa a saka zare a cikin kowane, a jera uku xaya-bayan-xaya sai a qulle zaren su yi kusurwa uku, sai a saka azzakarin yaron a cikin waxannan ‘yankara tsakanin azzakarin da ‘ya’yan golayensa, a xaure da zaren ga qugunsa kamar ya sa jigida yadda ‘yankaran za su tallabo azzakarin yaron ya rabu da ‘ya’yan golayen. Amfanin ‘yankara wajen kaciya shi ne, domin su raba azzakarin da ‘ya’yan golayen kar su game.

Wannan bincike nasa yana da alaqa da bincikena domin ya yi magana a kan kaciya, kuma ya taimakeni na gane kaciyar qasar Hausa.

Sannan mun bambanta a da’irar bincikena a inda shi ya tsaya a kan kaciyar qasar Hausa, ni kuma nawa binciken ya tsaya ne a kan nazarin kaciyar Hausawa Kanawa da Larabawan Sebha na Libya.

Shanono (2006) ya gabatar da kundin bincike mai suna “Al’adun Shekara-shekara a qasar Hausa”. A cikin kundin binciken,

ya kawo bayanin kaciya da yanayinta a qasar Hausa kafin da bayan shigowar addini Musulunci, sannan ya faxaxa bayanai a kan yadda ake yin kaciya a qasar bayan shigowar addinin Musulunci da bayyana lokacin da Hausawa suke yin kaciya a al’adance da al’adun da ake aiwatarwa a dalilin kaciya, kamar sa ranar kaciya da haqa rami da bayyana abubuwan da wanzami yake zuwa da su domin yin kaciya, kamar qwaqqwaran zare da maganin gargajiya  da ake ba yaro ya sha da bayyana al’adar keve wa xankaciya xaki da ziyarar da wanzami ya ke wa xankaciya kowacce safiya, sannan ya bayyana abincin xankaciya irin su dafaffun kaji da soyayyu da yaji da manshanu. Idan kuma xankaciya ya sha kunun kanwa, to dole ne sai an baxa masa yaji. Har ila yau kuma, a kundin nasa ya bayyana yadda ake yi wa xankaciya karkiya tare da kawo waqoqin zolayar xankaciya.

Wannan binicke ya bani haske sosai na daxa fahimtar kaciyar qasar Hausa a al’adance da yanayin aiwatar da ita da al’adun cikinta da ire-iren waqoqin da Hausawa suke zolayar xankaciya da su.

Babale, (2008) ya gabatar da kundin bincike mai suna “Barkwanci tsakanin wasu masu sana’o’in gargajiya a qasar Hausa”. A cikin binciken nasa ya kawo asali da yanayin wasannan

da yake faruwa a tsakanin maqera da wanzamai, a inda ya kawo yadda wanzamai suke yin sana’o’insu ciki har da kaciya, sannan ya kawo yadda wasannin yake gudana a tsakanin wanzamai da maqera.

Wannan bincike ya qara ba ni hasken sanin aikace-aikacen wanzamai musamman kaciya da kuma fahimtar al’adun barkwancin wanzamai da wasu masu sana’o’in gargajiya a qasar Hausa musamman maqera.

Yakubu (2008), ya gabatar da kundin bincike mai suna “Qaramin Qamus na Kevavvun Kalmomin Wanzanci”. Wannan bincike ya kawo bayanan masana al’ada irin binciken (Sallau, 2009) da (Almajir, 2010) da (Vatagarawa, 2010) a kan wanzanci, sannan aka zavi kalmomi da yawa masu alaqa da wanzanci aka yi bayaninsu.

Wannan bincike ya bani haske sosai a kan daxa fahimtar sigogin wanzanci da mafi yawan aikace-aikacen wanzamai da kuma daxa fahimtar kaciya da al’adunta a qasar Hausa.

Haka kuma Sallau (2009), ya gabatar da bincike a kundin digirinsa na uku mai suna “Sana’ar wanzanci da sauye-sauyen zamani jiya da yau” a cikin wannan bincike ya yi bayani ne kamar haka:

Ya kawo bayanin kaciya a qasar Hausa da yadda al’adun kaciyar yake ya kawo bayanin kaciyar sa-wandonka, ya yi bayani sosai da misalai.

Wannan bincike yana da alaqa da nawa binciken ta vangaren kaciya a qasar Hausa, domin ya yi bayani sosai a kan yadda ake yin kaciya a qasar Hausa.

Sannan mun bambanta a kan iyakancewar bincike, domin nasa binciken ya tavo bayanin kaciyar Hausawa ne kawai.

Ni kuma nawa binciken zai taqaita ne a kan nazarin al’adun kaciyar Hausawa Kanawa da Larabawan Sebha a Libya.

Sannan wannan binciken nasa ya taimake ni sosai, wajen sanin yadda Hausawa suke yin kaciya da yadda suke aiwatar da al’adar kaciyar.

Nihal, Taha (2009) ta bayyana a cikin kundin bincikenta mai suna الشعبي في محافظة رام الله الطقوس والمعتقدات الشعبية والاجتماعية في الادب wato “Yin ibada da sanin al’amuran rayuwa cikin adabin mutanen garin Ramalla a qasar Falasxinu”.Wannan bincike na Nihal (2009) ya kawo tarihin qabilu daban-daban a duniya waxanda suke yin kaciya musamman qabilun Misrawa da kuma Yahudawa a inda ta bayyana ta bayyana cewa suna yi wa yara kaciya daga shekara

shida zuwa shabiyu (6-12) kuma ana yinkaciyar ne a wuraren da ake yin bauta. Ta kuma bayyana cewa ba dole ba ne yin kaciya a garuruwan Yahudawa sai wanda ya ke so ne zai yi wa xansa.

Wannan bincike na Nihal ya taimake ni sosai wajen samin al’adun kaciya na mutane daban-daban a duniya, musamman Larabawa domin a kansu ta fi yin bayani.

Halima (2012) ta gabatar da bincike a kundin digirinta na biyu mai suna “Tasirin Al’adun Hausawa a kan Ibira a Kano a yau”. A bincikenta ta kawo tasirin da al’adar kaciyar Hausawa akan al’ummar Ibira, a inda ta kawo canje-canje da aka samu a kan al’adar kaciya a wajen Ibira bayan sun haxu da Hausawa, saboda cewa ta yi su al’ummar Ibira suakn yi wa ‘ya’yansu kaciya ne tun suna jarirai, wanda su Hausawa sai yaro ya kai shekara bakwai (7) a duniya. To yawanci al’ummar Ibira sun canza zuwa yadda Hausawa suke yi wa ‘ya’yansu kaciya, sai dai a yanzu saboda canzawar al’amura ba a bari yaro ya kai waxannan shekaru.

Wannan bincike ya taimakeni domin na fahimci yadda al’adun kaciya suke na gargajiya a wajen Hausawa, na kuma fahimci yadda suka yi tasiri wajen kawo sauyi a cikin al’adun

kaciyar al'ummar Ibiri a Kano, saboda hulxarsu da Hausawa mazauna Kano.

Doguwa (2013), ya gabatar da kundin binciken digiri na biyu mai suna "Kwatancin Ala'adun Haihuwa na Hausawa da Kurama a kudancin Kano da gabashin Zazzau". A kundin binciken nasa ya kawo bayani a kan asalin sana'ar wanzanci da yadda Hausawa suke aiwatar da ita tare da yin bayanin ire-iren ayyukan wanzamai da kayan aikinsu.

Wannan bincike ya daxa samin fahimtar yadda Hausawa suka xauki sana'ar wanzanci da aikace-aikacen wanzamai musamman kaciya.

Yahaya (2014) a kundin digirinsa na xaya mai suna "Kimiya da Fasahar Bahaushe Kafin Zuwan Turawa Qasar Hausa" a cikin bincikensa ya kawo bayanin ayyukan wanzamai, inda ya yi bayanin kaciya cewa tana xaya daga cikin ayyukan wanzamai a qasar Hausa, ya kawo kayayyakin aikin wanzamai a qasar Hausa, ya yi bayaninsu.

Wannan binciken ya daxa ganar da ni ayyukan wanzamai a qasar Hausa, musamman kaciya, bincikensa ya taimakeni wajen daxa fahimtar ayyukan wanzamai a qasar Hausa musamman kaciya.

**7.5.2 Bugaggun Littattafai**

A qoqarin samun bayanan da za a gudanar da wannan bincike an yi bitar littattafai da dama, waxanda suke xauke da bayanan da za su qare wa wannan nazari haske, littattafan da aka yi bita a wannan bincike su ne:

Madauci da wasu (1968), sun wallafa littafi a cikin harshen Turanci mai suna *Hausa Customs*. A inda ya kawo bayanin kaciya a qasar Hausa da yadda ake aiwatar da ita da yadda ake sa magani da yadda ake yin karkiya da ‘yar kara da yanayin al’adun wanzamai na ziyartar xankaciya a kowacce safiya da bayyana ire-iren abincin da xankaciya yake ci na daga kaji da yaji da kunun kanwa da kuma al’adar ware masa xaki don yin jiyar kaciyarsa. Sannan ya yi bayanin yadda ake yi wa yara kaciya a tare lokaci guda a qasar Hausa.

Wannan littafi ya daxa fahimtar da ni yadda Hausawa suke aiwatar da kaciya da yanayin gudanar da al’adun kaciya tun daga shirye-shiryen yinta zuwa warkewarta.

Abu Buzid (2009:113-115) a cikin littafinsa mai suna ومضات من التراث الليبي

Wato: “Haska Al’adun mutanen Libya”

Ya yi bayani a kan kaciya, ya kuma bayyana shekarun da ake fara yi wa yaro kaciya wato biyu, ya faxi al'adun kaciya na gargajiya a wajen Larabawa, kamar rufa wa yaro tsofaffin tufafi, waxanda aka adana domin yin kaciya, za a sa masa zannuwa masu xauke da rubutun Allahu Akbar, sannan a kawo kwano (akushi) a ajiye a gaban yaron, sai mai yin kaciyar ya zo ya yi wa yaron kaciyar.

Marubucin ya ci gaba da cewa akwai waqa, wadda mata suke yi wa yaro a lokacin yi masa kaciya wato:

"طهاره نعولوافيه - جميع لبينّا حاضرينه
إن شاءالله بعد (طهور)- على فراش لولاف نقعدوا"

- Za mu haxu mu yi hidima mu kyauta wa al'ummar da suke wurin nan
- In sha Allahu idan an (gama kaciya) za mu shimfixa tabarma mu huta.
- Sannan a mayar da yaro gurin mahaifiyarsa cikin farin ciki.

Wannan littafi ya yi matuqar taimaka min, wajen sanin yadda Larabawan Sebha suke aiwatar da kaciya a gargajiyance, kuma zai taimake ni sosai a wanan bincike da nake gabatarwa, littafi ne wanda ya ba ni haske sosai na yadda zan fahimci kaciyar gargajiya a wajen Larabawan Sebha.

Musa (2008:12) a cikin littafinsa mai suna "الادب الشعبى وثقافه في المجتمع" wato “Adabin jama’a da al’adunsu gaba xaya” ya kawo waqar da ake yi wa xankaciya a al’adar Larabawa, wato a cikin waqar ake kawo hoton yadda ake gudanar da kaciyar da kuma al’adun kaciyar da ake yi, kamar hoton yadda ake yin kaciyar ake kawo wa a waqe, sannan ya bayyana cewa a cikin waqar ana ambatar sunan yaron da ake yi wa kaciyar (shayin) da sunan mahaifiyar yaron da mahaifinsa (ubansa) da kuma wasu daga cikin ’yan’uwansa, sannan ana ambatar sunan wanzamin da yake yin kaciyar, marubucin littafin ya kawo misalin waqar da ake yi wa xan kaciya a lokacin yi masa kaciyar, kamar haka:

مطاهرناالصغيرعالى – وأسنان اللبن في فمه
وبشويش عليه يا مزين – وأنت بتحضنه وضمه

Iyalin yaron nan suna sonsa sosai,
Kamar madara ce a cikin bakinsa.

Wanzami ka yi masa a hankali a hankali,
Sannan ka rungume shi sosai.

Sannan iyalin yaron da ake yi wa kaciyar sukan zamo ’yan’uwan yaron da ake yi wa kaciyar na jini, sannan mata sun fi yin waqar.

Wannan littafi yana da alaqa da bincikena, domin ya tavo bayanin yadda Larabawa suke yin kaciyarsu ta gargajiya, wannan

littafi ya taimake ni sosai, saboda na samu bayanai da yawa a cikinsa, waxanda za su taimake ni na gudanar da wannan bincike nawa. Sai dai shi ya yi bayani ne a kan kaciyar Larabawan kawai ta gargajiya, ni kuma nawa binciken zai tavo har kaciyar gargajiya wacce ake yinta a birnin Kano na Nijeriya, birnin da in dai ana maganar Hausawa to dole a sa shi a ciki.

Abu Kiresha (2002:154) a cikin Littafinsa mai suna “ تأملات فى الواقع الأجتماعي المصري" wato “Tunanina a kan halayen mutanen Masar” marubucin ya yi bayani loakcin da ake yi wa yaro kaciya, domin kar ya sha wahala a al’adar Larabawa, ya kawo bayanan yadda wanzamai suke yi wa yara domin kar su ji zafin kaciyar da ake yi musu kamar haka:

Da farko wanzami zai ja fatar azzakarin yaron sai ya xaure ta da zare, sai ya cire da sauri ta amfani da aska ko almakashi, sannan za a kawo duwatsu a sa su a cikin ruwa, har tsawon kwana uku (3) a ba wa yaron ruwan ya sha, ya kuma yi wanka da sauran. Haka kuma za a kawo kwano na tangaran (na qasar Cana) a kakkarya shi, a kuma niqa shi sosai, har sai ya zama kamar gari (fulawa), sannan a sa wa yaron da aka yi wa kaciya a cikin azzakarinsa. Har ila yau za a kawo zare baqi, wanda aka yi da auduga a toye shi a sa wa yaron da aka yi wa kaciya a cikin azzakarinsa.

Marubucin ya bayyana cewa; waxannan magungunan za su sa yaron da aka yi wa kaciya (xankaciya) ya warke da sauri, bayan an yi masa kaciya.

Wannan littafi yana da alaqa da binciken da nake gadanarwa, saboda littafin ya yi bayani sosai a kan al’adun da Larabawan Sebha mazauna Libya suke yi a lokacin yi wa yaro kaciya, wannan littafi ya taimake ni sosai a fahimci al’adun kaciya na gargajiya a wajen Larabawan Sebha na qasar Libya, kuma bayanan za su yi matuqar amfani a aikina, sai da shi marubucin shi a littafinsa ya taqaita bayanansa ne a kan al’adun kaciyar gargjaiya ta Larabawa, ni kuma nazarin da nake yi ya faxaxa ne har da nazarin kaciya a wajen Hausawa na har da nazarin kaciya a wajen Hausawa na birnin Kano da ke Nijeriya, baya ga na Larabawan Sebha da ke Libya, amma na amfana da littafin sosai, kuma zai taimake ni a wannan binciken da nake yi a yanzu.

Gunaimm (2005:208) a cikin littafinsa mai suna "العادات والتقاليد في دلتا مصر" wato “Al’adar Kaciya a Garin Delta na Qasar Masar”.

Marubucin ya yi bayani game da bikin kaciya da cewa bikin kaciya ya sami karvuwa ne a wajen dukkanin Larabawa

talakawansu da masu arzikin cikinsu, ya bayyana cewa mai yin kaciya kuwa ana kiransa da sunan (muzayin) wato wanzami kenan, idan aka zo wajen gudanar da bikin kaciya, asu yin bikin za su shirya babbar walima, su gayyace dukkanin ’yan’uwa da abokan arziki, haka kuma duk ’yan’uwan wanda aka yi wa kaciya, suna zuwa ne tare da tsarabarsu. Wannan tsarabar da ake bayarwa mafi yawa kuxi ne ake a je shi a cikin xan wani kwano da wanzami ya ke amfani da shi. Bugu da qari wannan al’ada ana samunta har yanzu a wajen Larabawan Misira tun kafin zuwan addinin musulnci tun wajen shekara (440) kafin zuwan Annabi Isa suke amfani da ita har zuwa yau. Haka ma somariyin da Fini-fawa sun karvi wannan al’ada daga cikin Misrawa haka ma Habashawa su ma sun karvi wannan al’ada, sannan mashahurin masanin tarihin nan Hirodotss ya bayyana cewa: har yanzu al’ummar Misra ana samun wannan al’adar a wajensu.

Wannan littafi ya taimake ni sosai na daxa samin al’adun gargajiya na kaciya a wajen Larabawa, sannan bayanan za su taimake ni a bincikena, sai dai shi ya taqaita sana nazarin ne a kan al’adun kaciya na gargajiya a wajen Larabawa, amma ni nawa nazarin zai haxa da nazarin al’adun kaciya na gargajiya a wajen

Larabawan Sebha na qasar Libya da Hausawa na birnin Kano da ke Nijeriya, amma na qaru sosai da bayanan cikin littafinsa, kuma za su taimake ni a wannan nazari nawa, musamman idan na zo yin byanin al'adun gargjaiya na kaciya a wajen Larabawan Sebha da ke qasar Libya.

Al-Kashat a cikin littafinsa mai suna: "التراث الشعبي العربي الليبي" wato "Al'adun Larabawan qasar Libya" (2006:53) ya bayyana hadda ake yin kaciya a qasar Libya da cewa ba a shekara da yaro ake yi msa kaciya amma ana iya yi masa kaciya tun yaro yana shekararsa ta farko a duniya har zuwa shekara bakwai. Haka kuma ya ce qasar Libya ana yi wa yaran maza kaciya ne kawai kuma wannan al'ada ce ta larabawa mazauna arewacin Afrika. Amma a qasar Misira da Sudan suna yi wa mata ma kaciya. Wannan kuwa yana xaya daga al'adun larabawa na da. Ranar kaciya ana shirya babbar walima a kira 'yan'uwan da maqwabta. Aufa wa yaron da za a yi wa kaciya tufafi farare masu zane-zane, kuma ana zobuna a jikin tufafin da ke jikin yaron, sannan ana zana gida-gida kamar haka a jikin tufafin, ana tunani wannan zanen zobuna na Annabi Sulaimanu ne, ana kitse gashin yaro a yai masa jela mai tsawo a keyarsa guda xaya, sannan a qarshensa na xaure shi da qahon barewa.

Wannan littafi ya taimake ni sosai, wajen sanin al’adun kaciya a wajen Larabawan Sebha na Libya.

Bin Arafa (2010) a cikin littafinsa mai suna: “tarihi Fazan al-taqaifi wa al’ijtima’i manshura’at al-martaz alwatani illmafaxat wa al’dirasat al’tarihiya”.

Haka zalika ya yi bayani sosai a kan yadda ake yin al’adun bikin kaciya, inda ya ce: Bikin kaciya ya kasance wajen gudanar da shi akan gayyaci iyali da mutanen gida da maqwabta, yayin wannan biki ana rufa wa yaron da za a yi wa kaciya tufafi masu kyau da ado da zane-zane, mafiyawan lokuta yaron da ake yi wa kaciya bai san mai yake gudana ba da dalilin wannan taro ko kuma bikin, ba a sanar da shi don kada ya ji tsoro, amma ana mailalle a hannayensa da kuma qafufansa sannan kuma ana ba shi tsaraba kamar “qwai” da “al’kaki” kuma duka abin da yaro yake sha’awa ba tare da saninsa ba, sai wanzami ya shigo ya yi mayaro kaciya da sauri, wasu daga cdikin ’yan’uwansa mutum xaya ko biyu sun riqe shi bayan an gama sai uwar yaro ta yi guxa da kuma waqa tare da matan da suke tare da ita kamar haka:

طهّريامطهّر – صح الله إيديك
ولاتجرحلى الغالى – عزم أمه رقيق

- Wanzami ka yi wa yaro kaciya, - Allah ya saka maka.
- Ka yi hankali kar ka ji masa ciwo ya masoyina–zuciyar uwarsa mai rauni ce sosai.

Rafi’u (1981:94) a cikin littafinsa mai suna “ مكة في القرن الرابع عشر للهجره" ” wato: “Garin Makka a cikin qarni na goma sha huxu (14)” cewa ya yi kaciya na nufin tsabta sannan ya ci gaba da cewa: “sai yaro ya kai shekara biyu har zuwa biyar ake yi ma kaciya.

Kafin wanzami ya zo, ana rufewa yaro tufafi masu kyau da zane-zane a kuma naxa masa guntun rawani a kansa, sannan a hau da shi kan doki a zagaya da shi a garin (wato garin da yaron ya ke) ya yi ziyarce-ziyarce sai ai masa kaciya.

Haka kuma magarabi (1982:163) a cikin littafinsa mai suna “مراحل الحياة الاجتماعية في القرن الرابع عشر” wato “Rayuwar mutanen garin Hajaz a qarni na goma sha huxu (14)” shi ma cewa ya yi al’adar Larabawa yawanci sai yaro ya kai shekara uku zuwa huxu ake masa kaciya, sannan ’yan’uwan yaro da maqwabta suke hallara wajen yin kaciya. Haka kuma, bayan an yi ma yaro kaciya sai ’yan’uwa su ba wa yaro tsaraba.

Bagafar (1987:101) a cikin littafinsa mai suna “رباط الولايا” wato “Haxakar garuruwa” cewa ya yi a birnin Jidda na qasar Saudi ana yi wa yaro kaciya idan shekarunsa sun kai uku zuwa huxu,

kuma wanzami ne yake yin kaciyar bayan an gama kaciya sai a shirya masa babbar walima.

Al-hamami (1971:97) a littafinsa mai suna “ الأزياء الشعببه والثقافية في سوريا” wato “Sutturun mutanen siriya masu kyau ya bayyana mana yadda ake yin shayi (kaciya) qasar Siriya da cewa; ana rufawa yaro rigar (Al-hariri) fari da barnusi fari shi ma na (Al-hariri) ba tare da wando ba. Ana rataya wa yaron sannan a yi masa qunshin (Al-kamoon) a wuyansa don ya tsare shi daga kowane irin iskoki. Haka kuma za a rufa masa kula a kansa mai zane-zane da kuma duwatsu masu qyalqali, ana sa masa zobe da takalma.

Waxannan littattafai na Rafi’u (1981) da magarabi (1982) da Bagafar (1987) da Alhamami (1987), sun taimake ni sosai wajen sanin al’adun Larabawa a wajen kaciya, kuma za su taimaka wa aikin bincikena sosai.

Madabo (1979) ya rubuta littafi mai suna *Ciniki da sana’o’i a qasar Hausa*, a cikin wannan littafi ya kawo ma’anar wanzanci, ya kawo kayan aikin wanzanci waxanda suka haxa da: tankolo, zabira, aska, qaho da sauransu, ya yi bayanin al’adun wanzamai waxanda da suke haxa da kishi da hamayya da nuna gwaninta da kuma ladabi da taimako a wasu lokuta har da roqo.

Wannan littafin ya taimakeni wajen daxa fhimtar ayyukan wanzamai a qasar Hausa, musamman kaciya, sannan ya taimakeni wajen sanin al'adun wanzamai musamman a lokacin yin kaciya a qasar Hausa, wannan littafi zai taimaki wannan bincike da nake yi da bayanai sosai, domin ya bani bayanai masu muhimmanci a kan yadda aikin wanzanci yake a qasar Hausa.

Gusau (2015) ya rubuta littafi mai suna *Mazhabobin ra'i da tarken adabi da al'adu na Hausa*. A cikin littafin ya kawo mazhabobi da ra'o'i na nazarin adabi da al'ada, waxanda masana suka kawo domin masu bincike na ilimi su yi amfani da su.

Wannan littafi na Gusau (2015) ya taimakeni sosai domin a cikinsa nba samu ra'in da zan yi amfani da shi a wannan bincike nawa, wato: mazhabar sassarquwar al'adu wadda Gusau (2015) ya kawo a shafi na arba'in da biyar zuwa arba'in da shida a cikin littafin (45-46).

Sallau (2010) ya rubuta littafi mai suna: *Magani a sha a yi Wanka a Buwaya* a cikin littafin ya kawo bayanin magungunan wanzamai da tsatsube-tsatsube da sihirce-sihircen wanzamai, a inda a shafi na sittini da uku (63) na littain ya yi bayanin yadda wanzami suke yin asiri su mayar da kaciya sabuwa fil.

Wannan littafi na Sallau (2010) ya taimakamin wjaen sanin yadda wanzamai suke yiin asiri a kan kaciya a qasar Hausa, kuma wannan littafi zai tiamaki bincikena sosai domin ya kawo bayanin kaciya da al’adunta a qasar Hausa sosai.

Sallau, (2010) ya rubuta littafi mai suna *Wanzanci da Muhimmancinsa ga Rayuwar Hausawa*. a cikin littafin ya yi bayanin qasar Hausa da Hausawa da hanyoyin tattalin arzikin Hausawa, sannan ya yi bayanin asalin sana’ar wanzanci da rabe-raben wanzamai a qasar Hausa, ya kawo kayan aikin wanzani a qasar Hausa, sannan ya yi bayanain aikin wanzancin jini a ind aya yi bayanin kaciya a gargajiya da bikanci da kuma matsayin kaciya a addinin Musulunci, ya yi bayanin yadda wanzamai suke yin kaciya a qasar Hausa, ya kawo bayanin yadda ake bikin kaciya a qasar Hausa, ya kawo kayayyakin da ake yin amfani da su a wajen yin kaciya.

Wannan littafi yana da alaqa ta kusa da binkena, domin ya fayyace komai da ake so a sani a kaciya da al’adun da Hausawa suke yi a wajen yin kaciya, wannan littafi ya taimakine sosai a wannan bincike da nake gudanarwa.

### 7.5.3 Muqalu da Takardun Ilimi

Haka kuma a qoqarin tattaro bayanan da za su tallafi wannan nazari da ake son gudanarwa ya kai ga nasara, an yi bitar muqalu waxanda masana da manazarta suka gabatar kamar haka:

Satatima (2012) ta gabatar da maqala mai taken "Patronage of 'sa wando' Circumcision Pratice in the Metropolis of Kano: Traditional or Modern?

A cikin wannan maqala ya gabatar da shekarun da yaro ya ke kaiwa a yi masa kaciya a qasar Hausa, wannan bincike nasa ya kawo taqaitaccen bayani a kan garin Kano da qwaryar birnin Kano, ya kawo abubuwa guda shida (6) waxanda wanzamai suke amfani da su a gargajiyance idan za a yi kaciya wato:

Aska da Qyalle (qaramin yadi) da Auduga da lilo da Almakashi na gargajiya da Itacen masara (karkiya) da kuma maganin gargajiya

Satatima (2012) ya karkata bayaninsa a kan yadda ake aiwatar da kaciyar-sa-wando a qwaryar binnin Kano, ya kawo kayayyakin da ake amfani da su, waxanda ake haxa wa da na gargajiya a yi kaciyar sa wando wato: "Sifirit da Magani na shafawa da Reza da Almakashi na zamani da na gargajiya da Allurar da take maganin kamuwa da cuta da Auduga ta zamani".

Sannan ya kawo yadda likotoci suke yin kaciya asibitocin qwayar a birnin Kano, sannan ya kawo kayayyakin da likitoci suke amfani da su a  asibitocin qwayar birnin Kano.

Sannan ya kawo hanyoyin da ya bi wajen gudanar da bincikensa, wannan nazari yana da alaqa da bincikena domin ya fayyace abubuwa da dama na yadda kaciya take musamman ta sa wando da kuma kayayyakin amfani da yayin gudanar da kaciya, saboda haka wannan maqala ta Satatima (2012) ya taimakeni sosai wajen daxa fahimtar yadda kaciya take a qasar Hausa musamman a Kano, a inda ni nawa binciken ya zamo na al’umomi biyu wato larabawan Sebha na Libya da Hausawa mazauna Kano kuma binciken nawa ya shafi al’adar kaciya ta gargajiya ne, shi kuma nasa binciken a kan kaciyar sa wando a qwaryar birnin Kano ya gabatar, amma ya qara min haske sosai a kan yadda zan gudanar da bincikena.

Ahmad (2013) ya gabatar da muqala mai taken “Al’adun mutane”. A cikin muqalar ya yi bayanin al’ada a cikin addinin Musulunci, a inda ya yi bayanin kaciya a Musulunci, sannan ya yi bayanin bambance-bambance da ake samu a tsakanin qabilun larabawa a game da kaciya, ya yi bayanain yadda ake aiwatar da

shirye-shiryen walima ga iyalin yaran da aka yi wa kaciya, musamman a yammacin qasashen larabawa, sannan ya yi bayanin al’adu da Larabawa suke yi a wurin yin kaciya, kamar yi wa yaro ado da lalle a hannunsa, sannan a hau da shi doki a zaga gari da shi, wannan al’ada a kan samu xan bambanci tsakanin gari zuwa gari.

Wannan maqala tana da alaqa da aiki na domin ta yi bayanin yadda Larabawa suke aiwatar da al’adun kaciya a gargajiyance, saboda haka wannan maqala ta taimakeni sosai wajen fahimtar al’adun Larabawa na kaciya, kuma za ta taimakeni sosai a wannan nazari da nake gudanarwa.

A wannan babi an yi bayani ne a kan tarihin Kano da tarihin garin Sebha da bayyana ma’anar kaciya daga masana da manazarta da kawo bayanan masana da manazarta a kan asali da tarihin kaciya a duniya da wajen Hausawa Kanawa da kuma wajen Larabawan Sebha na Libya. Sannan an yi bitar kundayen bincike waxanda suka haxa digiri na xaya da na biyu da kuma na uku, waxanda bitarsu ta tallafi wannan nazari nawa ya kai ga nasara. Haka kuma an yi bitar bugaggun littattafai da muqalu waxanda masana da manazarta daban-daban suka yi gabatar, bitarsu ta tallafi wannan nazari ya kai ga nasara.

# BABI NA UKU

## 8.0 RA'I DA DABARUN GUDANAR DA BINCIKE

Ra'i na nufin ganin dama ko ra'ayi (C.N.H.N: 364) shi kuwa (Gusau 2015: vii) ya bayyana ma'anar ra'i a nazari da cewa: Wasu matakai ne waxanda za a iya xorawa a lura ko a hango mahangar adabi ko al'adu. Kuma mazhaba takan qunshi bayanai ko tsinkaye-tsinkayen manazarta ko masana dangane da ainihin qwarangwal na wani matani ko wani aiki na fasaha ko na walwalar al'umma.

A wannan babi za a kawo ra'i da dabarun gudanar da wannan bincike. A babin an yi bayanin ra'in da aka yi amfani da shi a wannan bincike, sannan sannan an kawo hanyoyin da aka bi aka gudanar da wannan bincike. Ga su kamar haka:

### 8.1 Ra'in da aka Xora Wannan Bincike

A wannan bincike an zavi a xora shi a kan ra'in sassarquwar al'adu, saboda wannan ra'i yana magana ne a kan nazarin mabambantan al'adu na mabambantan al'ummomi.

Wannan ra'i an same shi ne a Gusau (2015: 45-46), wanda ya assasa wannan ra'i shi ne Farfesa Edward Twitchell Hall, wanda wani fitaccen masani ne wanda ya rayu daga 1914 zuwa 2009. Ya fara gabatar da wannan ra'i ne a littafin da ya rubuta mai suna *the*

*silent language* a 1959. Bisa yawanci, Hall ya yi rayuwarsa a Amerika ne.

Wannan mazhaba ta sami karvuwa a Amurka da kuma Jafan. Mabiyinsa na qut-da-qut shi ne George L. Trager wanda suka wallafa littafin *the analysis of culture* 1953 a tare da shi.

A shekarar 1950 Hall ya yi aiki da rundunar sojojin qasar Amerika a matsayin shugaba mai lura da makarantun qasashen waje, ya koyar da haxakar al'adu da yanayin sadar da su ga al'ummar qasashen waje. Edward Hall ya lura da yadda ake samun sadarwa a tsakanin al'ummomin saboda bambance-bambancen al'adu, sai ya yi qoqari ya samar da yadda za a iya bambance abubuwan da za su iya zama hanyar magance rashin fahimtar da ke tsakanin fahimtar sadarwa a tsakanin al'ummomi mabambanta saboda bambancin al'adu.

Wannan mazhaba ta sami karvuwa a Amurka da kuma Japan. Mabiyansa na qut-da-qut shi ne George L. Trager wanda suka wallafa littafin *the analysis of culture* 1953 a tare da shi. Sauran mabiyan Hall (1914-2009) sun haxa da:

**Daga Amurka**

- Richard D. Lewis
- Juisi V. Koisisito

- Geert Hofslede
- Califford Clorke
- da sauransu

**Daga Japan**

- Maslo Kunibiro
  ya fassara littafin Hall (1959) zuwa Jafananci
- Mitsuko Saito
- Yoshitaka Mike
- da wasu mabiyan nasa waxanda Farfesoshi ne na fannin al'adu da kuma kimiyyar harshe.

Akwai muhimman abubuwa guda huxu (4) da wannan ra'i na Hall yake xauke da shi, wato:

1) Qunshiyar al'ada
2) Lokacin Aiwatar da Al'ada
3) Gurin Aiwatar da Al'ada
4) Saqon da ke Cikin Al'ada

➢ **Qunshiyar Al'ada**

A cikin qunshiyar al'ada Hall ya nuna za a lura da dokokin al'adar, ta lura da yadda ake furta ko aiwatar da al'adar da kuma manufarta, wato nazartar alaqar al'adu mabambanta na wasu al'ummomi, a inda ra'in nasa ya ta'allaqa ne ga lura da dokokin aiwatar da al'adar kowace al'umma.

- **Lokacin Aiwatar da Al'ada**

Hall ya bayyana lura da lokacin aiwatar da al'ada abu ne muhimmi wanda tantance kamanci ko bambancin yanayin aiki da al'adun mabambantan al'ummomi.

- **Gurin Aiwatar da Al'ada**

Hall ya zayyana yana kyau a lura da kowace irin al'ada a tantance guraren da suke aiwatar da al'adar, a inda za a fahimci al'adar da ko ta al'umma kaza ce, ko kuma ta yi kama ko kuma ace ta bambanta da al'adar al'umma kaza.

- **Saqon da ke Cikin Al'ada**

Hall ya bayyana yana da kyau a lura da yadda za a fahimci saqon dake cikin al'ada da kuma yadda za a isar da saqon daidai ga wasu al'ummomi na daban, har su fahimci abin da saqon dake cikin al'adar wata al'umma ta daban yake nufi, sannan su ma idan za su aiwatar da al'adar za su aiwatar da ita daidai ba tare da savawa abin da waccan al'ummar take nufi ko aiwatar da al'adarta ba, sannan za su fahimci kamanci ko bambancin aiwatar da al'adar wata al'umma da ta su al'ummar.

## 8.2 Ginshiqin Bayanai

Haqiqa akwai wasu muhimman bayanai waxanda aka yi amfani da su a wannan bincike waxanda suka taimaka qwarai wajen

samar wa wannan bincike muhimman bayanan da aka yi amfani da su, daga cikin hanyoyin da aka bi domin samo bayanan da aka yi amfani da su akwai:

### 8.2.1 Ziyarar Xakunan Ajiye Littattafai

A qoqarin tattaro waxannan bayanan an ziyarci xakunan karatu da dama, waxanda suka haxa da:

- Babban Xakin karatu na Jami’ar Bayero,
- Xakin karatu na Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya da ke Jami’ar Bayero,
- Cibiyar Bincike " منشورات المركز الوطني للمأتورات الشعبية " a garin Sebha a qasar Libya
- Xakin karatu a garin Tripoli na qasar Libya mai suna "مكتبة الفرجاني".
- Cibiyar bincike ta Jami’ar Bayero mai suna “Centre for the study of Nigerian Language and Forklore”.
- Babban xakin karatu na Sashen Harsunan Afrika a Jami’ar Ahmadu Bello Zaria.

### 8.2.2 Hira da Wanzamai

A yayin tattaro bayanan da aka yi amfani da su a wannan aiki, an samu damar tattaunawa gami da yin tambayoyi ga wanzamai. Kuma an yi musu tambayoyi kamar haka:

- Yaushe aka fara yin kaciya?

- Waxanne abubuwa ne kayayyakin aikin kaciya?
- Waxanne ire-iren magunguna kake bayarwa?
- Shin waxanne al’adu ne ake yi a wajen yin kaciya?
- Yaya ake yin kaciya?
- Waxanne al’adu ake yi bayan an gama kaciya an koma gida?

Ba shakka an samu cikakkun amsoshi daga waxannan wamzamai domin sun amsa dukkanin tambayoyin da aka bijiro musu, kuma an samu cikakkun bayanai waxanda da su aka yi amfani a yayin aiwatar da wannan nazari har ya kai ga ci.

### 8.2.3 Tattaunawa da Masana da Manazarta

An samu damar tattaunawa da masana da manazarta, domin samun bayanan da za su tallafi wannan nazari.

Kuma an yi wa waxannan masanan tambayoyi kamar haka:

1. Yaya kaciya take a al’adance a wajen mazauna qasar Libya ko Hausawa?
2. Yaya ake aiwatar da al’adun kaciya a wajen Larabawan garin Sebha da Hausa Kanawa?
3. Wane lokaci ake yin kaciya a al’adance?
4. Wane irin magani ake yi wa ’yan kaciya a gargajiyance?
5. Su waye suke yin kaciya a gargajiyance?
6. Shin me aka sani a kan kaciya da al’adunta?

Waxannan masana da manazarta sun amsa dukkanin tambayoin da aka yi musu kuma an samu cikakkun bayanai waxanda da su ne aka gudanar da wnanan nazari, ba shakka bayanansu sun taimaka qwarai ga wannan bincike domin sun haska min hanyar da na bi har wannan bincike ya kammalu cikin nasara.

### 8.2.4 Tattaunawa da Likitoci Masu Fixa a Asibiti

An samu damar tattaunawa da likitoci masu yin fixa a asibiti, musamman masu yin kaciya, domin samun bayanai a kan kaciya, waxanda za su taimaka wa wannan nazari

Kuma an yi wa likitocin waxannan tambayoyi kamar haka:

1) Yaya ake yin kaciyar asibiti?
2) Me ye bambancin kaciyar gargajiya da ta zamani?
3) Wane kaya ake yin amfani da su a lokacin yin kaciya a asibiti?
4) Wane magani ake ba wa Xankaciya a asitibi?
5) Nawa ake biya a yi kaciya a asibiti?
6) Wane lokaci aka fi yin kaciya a asibiti?

Suma likitoci sun taimaka min sosai wajen amsa dukkanin tambayoyin da aka yi musu, haqiqa an samu cikakkun bayanai daga waxannan likitoci waxanda suka tallafi wannan nazari har ya kammalu cikin nasara.

### 8.2.5 Tataunawa da Tsofaffi Maza da Mata

A qoqarin tattaro bayanan da za a yi amfani da su a wannan nazari, an samu damar tattaunawa da tsofaffi maza da mata a vangaren Larabawan garin Sebha da ke Libya da Hausawa mazauna garin Kano na Nijeriya, an tattauna da waxanda shekarunsu ya fara daga sittin (60) zuwa sama.

Kuma an yi wa tsofaffin tambayoyi ne kamar haka:

1) Me ka sani a cikin al’adun da ake yi in an yi kaciya ko kafin a yi kaciyar?
2) Yaya ake yin al’adun kaciya a garinku?
3) Yaya ake yin walimar kaciya a garinku?
4) Waye yake kai yaro wurin yin kaciya?
5) Me ake tanada a lokacin yi wa yaro kaciya?
6) Waye yake yin kaciyar gargajiya a garinku?

Tsofaffin suma sun taimaka qwarai dagaske wajen gudanar da wannan bincike domin sun amsa dukkanin tambayoyin da aka yi musu. Shi ya sa bayanansu suka zamo wasu ginshiqan bayanai masu miimmanci waxanda aka yi amfani da su kuma suka yi matuqar taimaka wa wannan bincike har ya kammalu cikin nasara,

ba shakka bayanan da aka samu daga wajen waxannan tsofaffi ya taimaka wa wannan nazari qwarai da gaske.

A wannan babi, an kawo ra'in da aka xora wannan nazari a kansa wato ra'in sassarquwar al'adu wanda Farfesa Edward Twitchell Hall ya qirqiro domin nazartar al'adu mabambanta. Haka kuma an yi bayanin hanyoyin tattaro bayanai waxanda aka yi amfani da su a wannan nazari, waxanda suka haxa da ziyarar xakunan ajiye littattafai da hira da wanzamai da tattaunawa da masana da manazarta da tattaunawa da likitoci masu fixa a asibiti da tattaunawa da tsofaffin mata da maza Larabawan garin Sebha na Libya da garin Kano na Nijeriya.

Haka kuma wannan bincike da aka gudanar an samu bayanai ne daga watan Fabrairu, 2016 zuwa Fabrairu, 2018.

# BABI NA HUXU

## 9.0 KAMANCI DA BAMBANCIN AL’ADUN KACIYA A BIRNIN KANO DA GARIN SEBHA A LIBYA

A wannan babi za a kawo kamancin al’adun kaciya waxanda Hausawa Kanawa da Larabawa Larabawan garin Sebha na Libya suke gudanarwa a lokacin da za su yi wa yaransu kaciya, sannan za a kawo bambance-bambance da ake samu a tsakanin waxannan al’ummomi guda biyu wato Hausawa Kanawa da Larabawan Sebha na Libya ta fuskar al’adun kaciya.

### 9.1 Al’adun Kaciya Waxanda aka Samu Kamanci a Tsakanin Hausawa Kanawa da Larabawan Sebha a Libya

Daga cikin al’adun kaciya waxanda aka samu kamanci a tsakanin Hausawa da Larabawan garin Sebha akwai waxannan:

#### 9.1.1 Kaciyar Jinya

Wannan kaciya ce wadda ake yi a qasar Hausa, kuma idan an yi kaciyar yaro (xankaciya) zai zauna har tsawon lokaci yana jinyar kaciyar, wani yakan xauki wata xaya, wani yakan kai har wata biyu ya danganta da jikian yaro wani yana da saurin warkewa wani kuma ba shi da saurin warkewa.

Sallau, (2013) ya bayyana cewa: “A qasar Hausa wanzamai ne suke yin kaciya, kuma an fi yin kaciya a lokacin sanyi. Dalilin yin ta a wannan lokacin shi ne, Hausawa sun

xauka ta fi saurin warkewa, kuma a wannan lokaci an kai ga amfanin gona abinci ya wadata. Wannan ne zai qara taimaka wa yaro da aka yi wa kaciya ya sami wadataccen abinci mai gina jiki yadda zai yi saurin warkewa. Kuma a wannan lokaci ayyuka sun fara yin sauqi. Za a sami wanda zai tsaya, ya kula da yaron da aka yi wa kaciya har su sami sauqi ba tare da sun yi wani mugun wasa wanda zai sa su yi fami a kaciyar da aka yi musu ba".

Irin wannan kaciya ta jinya wanzami kan zo ya dinga duba xan kaciya duk bayan kwana biyu ko uku ko ma sati, sannan duk zuwan da wanzami zai yi zai dinga bayar da magani har xan kaciya ya warke, kuma irin wannan kaciyar ba a sa wando sai an warke sosai (Salau, 2013:153).

Irin wannan kaciya ta jinya su ma Larabawan garin Sebha suna yin ta a gargajiyance wato idan an yi wa yaro kaciya, ana samun xakin da zai yi jinya kafin ya warke (Hira da Isa Mohammed) wannan kamanci ne.

### 9.1.2 Adadin 'Yankaciya

Sallau (2013:153) ya bayyana cewa lokacin da za a yi kaciya iyayen yara na unguwa xaya ko qauye xaya sukan yi shawara a

tattara yaransu wuri xaya don a yi musu kaciya, kuma ana tsayar da mutum wanda aka tabbatar yaran na tsoran don ya riqa kula da su har sai sun warke. Saboda haka a iya cewa a qasar Hausa ba a yanke adadin ’yankaciya, ya danganta da yawon yaran da za a yi wa kaciyar a unguwar ko qauyen, sannan kuma akan samu waxanda suke ware xansu su yi masa kaciya shi kaxai musamman a wannan lokaci da taimakekeniya ta yi qaranci a qasar Hausa.

A garin Kano kuwa, idan za a yi wa yaro kaciya ana kirawo wanzami ya zo gida ya yi wa yaro kaciya, amma yawanci a yanzu an fi xaukar yaron a kai shi gidan wanzami ko wani wani da wanzamin ya tanada domin aiwatar da sana’arsu ta wanzanci kuma ana iya haxa yara biyu ko uku ko sama da haka sa’annin juna a gida xaya a yi musu kaciya ko a unguwa xaya ya danganta da haxin kai da kuma zumuncin mutane (Hira da wanzami, Hassan Abubakar)

A garin Sebha ana samun wani mutum ya gayyato wanzami ya kuma sanar da mutanen unguwarsu cewa ranar kaza wanzami zai zo domin yi wa xansa kaciya, idan akwai wanda zai yi wa xansa kaciyar a wannan lokaci to wannan sanarwar ta zama an sanar da shi kenan, sai ya shirya ya kafa tuta a qofar gidansa wato alamar ya shirya yi wa xansa kaciya a wannan lokaci, wanzami zai zo gidan

mai masaukinsa (wanda ya gayyato shi) ya kwana a ranar Alhamis kasancewar al'adar mutanen garin Sebha a ranar juma'a suke yi wa 'ya'yansu kaciya, a ranar juma'a da safe duk wanda ya kafa tuta a gidansa zai xauko xansa ya kawo shi gidan da wanzami ya sauka domin a yi wa xansa kaciya, akan samu a qalla yara biyar (5) ko shida (6) amma ba sa wuce yara goma (10), koda-yake akan samu wanda zai gayyato wanzami ya yi wa xansa shi kaxai kaciya musamman masu kuxi[3].

Wannan kamanci ne na yadda Hausawa Kanawa da Larabawan garin Sebha suke yi wa 'ya'yansu kaciya a tare lokaci xaya.

### 9.1.3 Waqoqin Bikin Kaciya

A gargajiyance kafin a sami tasirin zamani, Larabawan garin Sebha suna aiwatar da wata al'ada kamar haka: Idan ya zama saura kwana biyu a yi wa yaro kaciya, sai 'yan'uwansa mata su fara biki kuma suna waqe-waqe da guxa, daga cikin waqoqin da suke yi akwai wannan waqar:

فرشنا الحصيره وغربلنا التراب

حضرنا وجه محمد والشيطا ن غا ب

[3] Hira da Aziza Alsugair, mazauniyar garin Sebha na qasar Libya.

A sa tabarma a tankaxe qasar nan
Mun fara ambaton sunan Annabi Muhammadu (SAW)
Shaixani sai ka bar wajen nan.

Daga an gama kaciyar sai mahaifiyar xankaciyar ta yi guxa sai ta fara waqa tare da matan da suka zo bikin, ga irin waqar da suke yi:

| | |
|---|---|
| طهر يامطهر | صح الله إيد يك |
| ولا تجرحلى الغا لى | عزم أمه رقيق |

Wanzami ka yi wa yaro kaciya,
Allah ya saka maka.

Ka yi hankali kar ka ji ma sa ciwo da masoyina,
zuciyar uwarsa mai rauni ce sosai.
(Bin Arafa, 2010:67)

A qasar Hausa kuwa, a al’adance bayan an gama kaciyar sai maroqa, wani lokaci ma har da maqaxa su sanar da mutanen da suka taru a wurin kaciyar cewa yaron ya girma. Daga cikin ire-iren kalaman da ke fitowa daga bakin maroqan na nuna an gama kaciya sun haxa da:

“A kawo kari yaro ya girma”
“A kawo karin kugunu”
“A kawo karin ba saukon daka”
“A kawo karin gama faxa, sa faxa”
“A kawo karin ta wando”
“A kawo karin abin ginar jarirai”

Daga nan ne sai dangi da abokan arziki su yi ta yi wa wanzamin da ya yi kaciyar da kuma yaron da aka yi wa kaciyar kyauta. Akan samu wasu yaran abubuwan da dangi suka tattara masu a lokacin da aka yi musu kaciya su zama dalilin arzikinsu. Domin kuwa wasu dangi da abokan arziki kan ba yaron da aka yi wa kaciya dabbobi waxanda sannu-sannu sai su yi ta yaxuwa har su yi yawa.

Bayan an gama bayar da kari sai a ci abinci, daga nan sai kowa ya koma gidansa. A yanzu irin wannan al'ada ta bikin kaciya an fara barin ta, sai wurare kaxan ne kawai ake yin wannan biki musamman a a qauyuka. Wannan kuwa ya faru ne saboda qarin wayewa da kuma rashin wadatar abin duniya ga mutane, wasu na nuna cewa wannan ya faru ne saboda qaruwar ilimin boko wanda ke qara sa zumunci tavarvarewa (Sallau, 2010:103-104).

Wannan kamanci ne na yadda ake samu waqe-waqe da kirare-kirare a tsakanin Hausawa da Larabawan garin Sebha a lokacin yi wa yara kaciya.

A garin Kano kuwa, kafin tasirantuwar zamani, idan an yi wa yaro kaciya ana yi masa wasu 'yan waqoqi na zolaya irin waxannan:

Xankaciya da warin tusa,
In ya buga gari ya waye bam!

Sannan akwai wata waqar zolayar kamar haka:

Xanshayi,
Ya ci qafar kare,
Bai qoshi ba,
Ya ci ta ungulu,
Gudu-gudu-gul a gidan biki.

A wata waqar kuma, a kan ce:

Xanshayi,
Ya ci qafar kare,
Bai qoshi ba,
Ya ci ta ungulu,
Da ta warke,
Gara ta guntule.

Ko kuma, a kan ce:

Na alemina,
Ya ci qafar kare.

Waxannan waqoqi na zolayar xankaciya akan yi su ne a lokacin da aka yi wa yaro kaciya bayan abokansa yara da sauran abokan wasansa kamar sakwanni da kakanni sun shigo gida domin duba shi ko kuma kawai domin su zolaye shi (Hira da Hassan Abubakar, wanzami a Kano).

### 9.1.4 Masu yin Kaciya Gargajiya a Kano da Sebha

A garin Kano, mutanen da suke yin kaciyar gargajiya su ne wanzamai waxanda suka gaji sana'ar wanzanci a wajen iyayensu.

Galibin wanzamai na yin wasu abubuwan bayan kaciya kamar cire beli da yin qaho da kuma yin aski, sannan har yanzu a garin Kano, jama'a da dama suna yi wa yaransu kaciyar gargajiya (Hira da Musa Zakariyya).

A bisa bincike an gano mutanen Kano sun fi yarda da kaciyar gargajiya wato wacce suka gada kaka-da-kakanni fiye da kaciyar asibiti musamman a qauyuka, amma yawanci masu ilimin zamani su kuma sun fi yi wa 'ya'yan kaciyar asibiti.

A garin Kano na Nijeriya akwai ire-iren kaciya kamar haka:

- Kaciyar gargajiya ta jinya
- Kaciyar gargajiya ta sa wando
- Kaciyar likiti ta zamani

Sannan yawanci wanzamai masu yin kaciya a garin Kano 'yan gado ne, domin Malam Hassan Abubakar wanzami, mazaunin unguwar Rijiyar zaki a garin kano ya shaida min cewa shi ma kakansa na wajen uwa da uba duk wanzamai ne kuma sarakan aska ne. Mahaifinsa shi ma sarkin aska ne, yayansa shi ma sarkin aska ne, saboda haka shi wanzanci musamman mai yin aikin kaciya sai xan gado, ita kuwa kaciyar asibiti, kowa yana iya yin ta idan ya yi karatun likitanci (Hira da Hassan Abubakar, wanzami a Kano).

Waxannan wanzamai masu yin kaciyar gargajiya a Kano, suna amfani da aska da magani ne kawai, kuma suna yin kaciyar ne a gidajensu ko wani shago da suka ware ko kuma mutum ya gayyace su zuwa gidansa don su yi wa xansa kaciya. Sannan yawanci a garin Kano, an fi yi wa yara kaciya a lokacin sanyi, wannan wata al'ada ce wadda ta somo saboda a lokacin kaka ce, akwai wadata a hannun mutane sakamakon zuwan amfanin gona, kuma ana tunanin ciwo ya fi warkewa a lokacin sanyi, wannan al'adar har yanzu ana aiwatar da ita a garin Kano (Hira da Malam Hassan Abubakar, wanzami a garin Kano).

Kaciya a wajen Hausawa Kanawa, aba ce mai matuqar muhimmanci, wadda tasirinta ya kai tun kafin zuwan addinin Musulunci qasar Hausa, akwai kaciya a wajen Hausawa Kanawa, sannan bayan zuwan Musulunci, sai ya qarfafesu da yinta (Hira da Salmanu Abdullahi wanzami a garin Kano).

A garin Sebha na qasar Libya kuwa wanzami ko Shehun Malami mahaddacin *Al'qur'ani* a cikinsu ake samun wanda zai yi wa yaro kaciya a gargajiyance, kuma har yanzu akan samu waxanda suke yin kaciyar gargajiya a garin Sebha musamman a qauyuka, sannan ana samun waxanda suke yin ta asibiti, musamman a cikin birni kamar yadda yake a garin Kano na Nijeriya.

Matsayin kaciya a wurin Larabawan garin Sebha, abu ne mai matuqar daraja, domin har ta kai a al'adar Larabawan garin Sebha, ba kowa ake ba wa yaro ya yi masa kaciya ba, sai amintaccen mutum dattijo ko wani mahaddacin *Alqur'ani*. Har ila yau wanzaman garin Kano da na garin Sebha, dukkaninsu tasirin zamani ya sa suna amfani da kayyakin yin kaciyar asibiti kamar auduga da maganin kashe zafi.

Wannan kamanci ne na masu yin kaciya a garin Kano da Sebha a Libya, a inda wanzami shi ne yake yin kaciya ta gargajiya a garin Kano da Sebha wannan kamanci ne. Kuma a yanzu zamani ya sa wanzamai a garin Kano da Sebha suna yin amfani da kayayyakin yin kaciyar asibiti wajen yi wa yara kaciya, wannan kamanci ne.

### 9.1.5 Kamancin Kayayyakin yin Kaciya a Kano da Sebha

Akwai wasu abubuwa waxanda wanzamai suke amfani da su a garin Kano da garin Sebha. Misali: wanzamai a garin Kano da garin Sebha suna amfani da waxannan abubuwa:

- **Reza**

Reza wata aba ce mai kaifi wadda turawa suka yo ta domin yanke-yanke na abubuwa ko yanke farce da sauransu. A garin Sebha wanzamai suna amfani da reza wajen yanke lovar kaciya, shi ya sa reza ta zama xaya daga cikin kayayyakin aiwatar da kaciya a garin Sebha, amma a Kano wanzamai su ma suna amfani da reza

wajen yanke-yanke ko kuma yanke wata ’yar qaramar fata da ta maqale a lovar kaciya, wato dai reza tana xaya daga cikin kayayyakin aiwatar da kaciya a garin Kano da garin Sebha na Libya.

- **Zabira**

Zabira jaka ce babba mai aljihuna da yawa misali uku ko huxu. Ana yi mata maratayi domin a riqa ratayawa. Ita ma dukawa ne suke xinka ta da fatar akuya ko tunkiya domin yi wa wanzamai jakar da za su riqa sanya dukkan kayan aikin wanzancinsu waxanda aka yi bayanansu a baya (Sallau, 2010:59).

Ita ma irin wannan jakar wanzaman garin Kano da wanzaman garin Sebha dukkaninsu suna amfani da ita wajen zuba zuban kayayyakinsu na wanzanci, wato dai wanzamai Larabawan garin Sebha suna amfani ne da jakunkuna iri biyu, ko dai su yi amani da tankolo ko kuma su yi amfani da zabira kamar yadda wanzaman Hausawa Kanawa suke amfani da duka biyun.

### 9.1.6 Xakin yin Kaciya (Wurin yin Jinya)

Idan an gama kaciya a qasar Hausa a garuruwa irin su Kano da sauransu, wanzami zai buxe jakarsa ya xauko matashi (wato

wasu ’yan karare ne waxanda tsawonsu bai fi tsawon xan quri ba da ake xauke da zaren abawa) sai a zura zakarin xan kaciya ciki. kararen sai su zauna tsakanin zakarin da kuma marainan xankaciya, sai kuma ya xauko shi ta qugun ko kwankwason yaron, ya kuma qulle shi. Daga nan sai wanzami ya xauko karkiya ya ce “idan yaron zai kwanta bacci sai a xaura masa domin ko da ya haxa qafafuwansa”. Daga nan sai ya xauko  magunguna na gargajiya ya bayar, ya ce “a dinga sa wa xankaciya a abinci ko ruwa ko koko”, daga nan sai a tashi xankaciya zuwa xakin da zai yi jiyya. ’Yan’uwansa mata da abokan wasa sai a yi ta zuwa ana duba xankaciya, ana kuma xan tsokanarsa. Al’ada ta tanadar wa xankaciya zama wuri guda, kamar xaki ko falo (Durumin’iya, 2006:58-59).

A yayin gudanar da wannan bincike, an fahimci cewa a garin Kano kuwa, idan an yi wa yaro kaciya, ana kai shi gida a dinga ba shi kulawa ta musamman, ta hanyar ba shi abinci na musamman kamar nama da kifi da madara da sauran girke-girken da ya ce yana buqata, kuma sau tari ana ware na xakin musamman da za a yi jinyarsa.

A garin Sebha kuwa ana ware wurin yin kaciya a gida sannan idan an gama yi wa yaron kaciya sai a ware masa wani xaki na musamman a gida kuma a qawata shi da shimfixu da fulo wanda za a kwantar da yaro a kansa (Hira da Mahammad Hassan Aliwa).

Wannan kamanci ne na yadda Hausawa Kanawa da Larabawan garin Sebha suke ware waje xaya domin yin jinyar xan kaciya.

### 9.1.7 Abincin Xankaciya

Durumin'iya(2006:59) ya bayyana abincin da xankaciya yake ci kamar haka:

- Naman kaji
- Zuma

Hausawa Kanawa suna ba wa xankaciya nau'o'in abinci kamar haka:

- Nama soyayye ko gasasshe na kaji ko na dabbobi
- Miyar kifi ko miyar nama
- Miyar ganye musamman ta taushe
- Sauran nau'o'in abinci kamar shinkafa da wake da tuwo da sauransu (Hira da Musa Zakariyya Rijiyar Zaki).

Su kuma Larabawan garin Sebha suna ba xankaciya waxannan ire-iren abinci:

- Naman kaji ko na dabbobi
- Qwai
- Madara (Nono)
- da sauransu

(Hira da A'isha Abdussalam).

Haqiqa akwai kamanci a abincin da ake ba wa xankaciya a garin Kano da garin Sebha a Libya domin Larabawan garin Sebha da Hausawa Kanawa suna ba wa xankaciya nama da kifi da nono wannan kamanci ne.

### 9.1.8 Lokutan Ziyara

Hausawa a al'adarsu da an yi wa yara kaciya sai 'yan'uwa mata da abokan wasa su yi ta zuwa suna duba xankaciya, suna kuma xan tsokanarsa, wanzamin a nasa vangaren zai riqa zuwa yana duba xan kaciya bayan kwana uku-uku ko sati-sati domin ganin ci gaban warakar xankaciya (Durumin'iya, 2006:59).

A garin Kano akan ziyarci xankaciya a waxannan lokuta kamar haka:

- Da hantsi (safe)
- Da yamma
- Da dare

Ba tsayayyen lokaci na kai wa xankaciya ziyara a qasar Hausa (Hira da Salihu Sani).

Su kuma Larabawan garin Sebha idan aka yi wa xan xan'uwansu kaciya sukan ziyarce shi domin duba lafiyarsa da ba shi gudummawa a waxannan lokutan da suka haxa da:

- Ana gobe za a yi wa yaro kaciya
- Ranar da aka yi wa yaro kaciya da safe
- Ranar da aka yi wa yaro kaciya da rana

Sannan 'yan'uwa da abokan arziki za su ci gaba da kawo wa xankaciya ziyara tare da kawo masa tsaraba ta wani abin daxi kamar nama ko nono ko zuma da sauransu (Hira da Aziza Alsugair).

Sallau, (2010) ya bayyana cewa: "A qasar Hausa bayan wanzami ya yi kaciya yakan riqa ziyartar yaran da ya yi wa kaciya domin ya ga idan akwai wata matsala da ke buqatar a gyara da kuma qara bayar da shawarwari, waxanda za su qara taimaka wa yaran su warke ba tare da fuskantar wata matsala ba. A lokacin da yaron ya warke, sai a sake gayyatar wanzamin domin ya zo wurin bikin wankan warkewar kaciya. A wurin bikin ya farko, sai wanzamin ya yi wa yaron aski, a yi masu wanka a kawo sababbin kaya a sanya masa".

Daga nan, sai ’yan’uwa da abokan arzikin iyayen yaron da aka yi wa kaciya su taya iyayen waxannan yara murnar ’ya’yansu sun warke lafiya, tun daga wannan rana waxannan yara sun shiga cikin harkokin ayyukan yau da kullum da ake yi a gidajensu, sai kuma a saya wa kowane daga cikinsu fartanyarsa don kuwa an yi masa bante. Idan an qara shekaru sai a fara nema masa aure. (Sallau, 2010:109).

Wannan ya nuna Hausawa Kanawa da Larabawan garin Sebha suna kai ziyara ga yaran da aka yi wa kaciya har su ba shi kyauta ta nama ko kaji ko qwai ko nono ko kuma kuxi, wannan kamanci ne.

### 9.1.9 Tufafin Kaciya

Hausawa suna xinka wa xankaciya sababbin kaya idan ya warke, sai ya sa kayan a haxa shi da wani ko wata a cikin ’yan’uwansa sai su zaga dangi ana nuna shi ana yi masa murna wato yaro ya girma, amma a vangaren lokacin da za a yi wa yaron kaciya ba dole ne a sa masa kaya sababbi ba, ana iya sa masa tsofaffin kayansa a wanke su a sa masa su a kai shi wajen wanzami ya yi masa kaciya ko kuma idan da hali sai a xinka masa sababbi (Hira da Musa Zakariya).

A vangaren suturar kaciya a garin Sebha kuwa tun a ranar farko ta fara bikin kaciya ake yi wa yaro wanka sannan a sa masa sababbin kaya wanda aka tanada a matsayin tufafin kaciya wannan tufafi ana xinka hula da zarurruka guda biyu wani lokaci har fiye da haka, ana yi wa hular ado da guntun qahon barewa da kuma dutsuna masu qyalli, za a sa kayan amshi da zahfaran (turare), sannan rigar da xankaciya zai sa doguwa ce, ana yi mata ado a gabanta da bayanta da zane-zane (Muhammad, 1998; sh. 41).

Wannan ya nuna Hausawa Kanawa da Larabawan garin Sebha dukkansu suna yi wa xankaciya sababbin tufafi, wannan kamanci ne.

**9.1.10 Gayyatar Kaciya**

Idan za a yi wa yara kaciya a qasar Hausa iyayen yaran na aika wa danginsu da abokan arzikinsu na kusa da na nesa, su sanar da su cewa za a yi wa wane kaciya a ranar kaza. Idan ranar ta zo dukkan dangi na kusa da na nesa da abokan arziki sai su taru a gidan domin bikin kaciyar. Iyayen yaron za su yi abinci, a kuma daka gero a yi garin da za a yi kunun kanwa wanda za a ba yaran da aka yi wa kaciyar (Sallau, 2010; sh. 103).

A garin Sebha kuwa ana gobe za a yi wa yaro kaciya za a samu ’yammata a danginsa su xauke shi su zagaya da shi ana

nuna shi a dangi ana sanar wa dangi cewa gobe za a yi masa kaciya, duk gidan da suka ziyarta za a ba su tsaraba, kuma za a yi musu addu'ar a yi kaciya lafiya, duk wacce aka je gidanta kamar an gayyace ta ne zuwa bikin kaciya, kuma za ta zo ne tare da 'ya'yanta da 'yan'uwanta, sannan za su taho da tsaraba, wato dai Larabawan garin Sebha suna yin bikin kaciya ne kafin a yi kaciyar zuwa lokacin da ake yi ta (Mohd, 1998:41).

Wannan ya tabbatar cewa Larabawan garin Sebha da Hausawa Kanawa suna gayyatar 'yan'uwa zuwa taya su murna yiwa xansu kaciya. Wannan kamanci ne.

## 9.2 Bambance-Bambancen da ake Samu a Al'adun Kaciya a Tsakanin Hausawa Kanawa da Larabawan Sebha a Libya

Daga cikin al'adun kaciya waxanda aka samu bambancin aiwatar da su a tsakanin Hausawa Kanawa da Larabawan Sebha, akwai waxannan:

### 9.2.1 Kaciyar Sa-Wandonka

Wannan kaciya qarin hikima ce da wanzamai a garin Kano suka samu a gargajiyance, wadda ake yi wa yaro kaciya da an gama, sai ya sanya wandonsa ya yi tafiyarsa yin harkokinsa na yau

da kullum. a irin wannan kaciya ba tsare yaro domin yin jinya kamar yadda ake yi kafin zuwan wannan hikima. A taqaice a iya cewa, kaciyar sa-wandonka ci gaba ne wasu wanzamai suka samu a gargajiyance.

Ita wannan kaciya babu wani bambanci wajen yinta da irin kaciyar da wanzamai ke yi, wurin sanya magani ne kawai bambancin yake. a wannan kaciya ba a tauna bagaruwa a furza ruwan, a maimakonta ana shafa ruwan magani ne mai mai, sai kuma a naxe kaciyar da wani farin qyalle kamar yadda ake yin kaciyar asibiti wannan farin qyalle da ake naxawa ba zai fita ba sai a lokacin da kaciyar ta warke (Sallau, 2010:110).

Irin wannan kaciyar ta Sa-Wandonka ba a yin ta a garin Sebha domin su wanzaman garin Sebha kaciyar jinya suka gada kuma ita ce kaciyar su ta gargajiya, duk da kaciyar sa-wandonka tasirin zamani ne ya kawo wa Hausawa Kanawa ita, amma ba ta je garin Sebha ba, saboda wanzaman Sebha ba sa yin ta. wannan bambanci ne.

### 9.2.2 Shekarun Kaciya

Sallau (2013:153) ya bayyana cewa a al'adar Hausawa sai yaro ya kai shekara bakwai ko fiye da haka ne za a yi masa kaciya,

amma ba a yi wa yaro kaciya yana da shekara takwas da haihuwa. Dalili shi ne an camfa don kuwa an xauka yin kaciya ga yaro a shekara takwas da haihuwa zai iya haifar masa da wani bala'i. wannan dalili ne ya sa idan ba a yi wa yaro kaciya a lokacin da yake da shekara bakwai da haihuwa ba, to ba za a yi masa ba sai ya kai shekara tara ko wuce tara da haihuwa. Amma a binciken da na yi a yanzu Hausawa Kanawa da dama sun ajiye al'ada suna yi wa yaransu kaciya daga matakin ko shekara uku ko huxu ko biyar ko yadda mutum yaga dama har shekara takwas da ba sa yin kaciya a al'adance.

A qasar Libya musamman Larabawan garin Sebha suna yi wa 'ya'yansu kaciya a gargajiyance, tun yaro yana da shekara xaya zuwa shekaru uku (1-3), wato mutum zai iya yi wa yaransa kaciya a shekara xaya ko biyu ko kuma uku, wannan su ne shekarun yi wa yara kaciya a garin Sebha na qasar Libya (Kaciyar gargajiya)[4].

Wannan ya nuna akwai bambancin al'ada a tsakanin Hausawa kanawa da Larabawan garin Sebha ta vangaren shekarun da kowace al'umma daga cikinsu ta amince ta yi wa yaro kaciya.

[4] Hira da A'isha Abdulsalam, mazauniyar garin Sebha na qasar Libya.

### 9.2.3 Ranar yin Kaciya

Durumin'iya (2006:58) ya bayyana cewa: "Bahaushiyar al'ada ta tanadi ranar juma'a ta yanayin na hunturu ko sanyi ta zamanto ranar da kuma lokacin da ake yin kaciya. Babu wani nafsi da ya zo da cewa dole sai a wannan ranar ne za a iya yi kaciya. Wataqila, Hausawa suna yin kaciya ne ranar Juma'a domin girmamata da kuma darajar do ranar take da shi a idanun Musulumi duniya. Amma dai mafi yawanci an fi yin kaciya ranar juma'a da xan'hantsi, a wannan rana, ana tuqa tuwon shinkafa miyar taushe, haka kuma 'yan'uwa mata sukan taru a gidan da za a yi wa yaran ko kuma yaro kaciya. Da sassafe, za a yi wa xankaciya wanka, sannan a zo a zaunar da shi a tsakar gida ko kuma shamaki ko soro wanda a nan ne za a yi kaciyar. Amma a yayin gudanar da wannan bincike, an gano Hausawa Kanawa suna yi wa yaransu kaciya a duk ranar da suka ga dama, amma har yanzu sun fi yi wa yaransu kaciya a lokacin sanyi, saboda tunanin zata fi warkewa da wuri.

A garin Sebha ana fara bikin kaciya ne ranar Alhamis, sannan ana xinka wa mahaifiyar yaron sabuwar riga da sabon takalmi da kuma bargo sabo, domin ta yi fitar bikin kaciya, a wannan ranar ta Alhamis uban yara (mahaifi) kan xauki yaro ya kai shi wajen

wanzami domin a yi masa kaciya, ana yi wa yara kaciya ne a wani kevavven wuri da wanzami ya ware a gidansa ko a wani wuri da aka ware a gidan su yaron da za a yi wa kaciya, bayan an gama yi wa yaron kaciya ana ba shi abubuwan sha’awa masu daxi kamar “kuskus” da “fitat” da “bazin” da sauransu (Mohd, 1998: 41).

Ana fara shirya walimar kaciya ranar juma’a, a inda za a girka tuwo da nama a tara maqwabta da ’yan’uwa a yi walima, wanzami zai zo gidan a wannan rana ta juma’a kuma a nan zai kwana, ranar Asabar ita ce ranar yin kaciya, ana yin kaciyar ne bayan sallar la’asar, ’yan’uwan xankaciya tsofaffi (maza) su ne za su raka yaro gurin da aka ware domin yin kaciya (Hira da A’isha Abdussalam, mazauniyar garin Sebha).

Idan muka duba waxannan bayanan da aka kawo za mu ga cewa Hausawa suna yin kaciya ne ranar Juma’a a al’ada saboda tasirin addini kamar yadda Durumin’iya (2006, sh. 58) ya bayyana, su kuwa Larabawan garin Sebha ranar Alhamis ko ranar Asabar suke yin kaciya a al’ada, sai dai a yanzu saboda zamani da Hausawa Kanawa da Larabawan garin Sebha suna iya yi wa yara kaciya kowace rana, amma a al’ada akwai bambancin ranar yi wa yara kaciya a tsakanin Hausawa Kanawa da Larabawan garin Sebha

wato Kanawa suna yi wa yara kaciya ranar Juma'a, su kuwa Larabawan garin Sebha suna yi wa yara kaciya ne ranar Alhamis ko Asabar a gargajiyance. Wannan bambanci ne.

### 9.2.4 Kayayyakin yin Kaciya

Akwai kayayyakin da wanzamai Hausawa Kanawa suke amfani da su waxanda wanzaman garin Sebha ba sa yin amfani da su wajen yin kaciya, waxannan abubuwa su ne:

- Aska
- Karkiya
- 'Yarkara
- Fatar Washin Aska

(Hira da wanzami, Salmanu Abdullah na garin Kano)

Su kuma wanzaman garin Sebha a gargajiyance suna amfani da almakashi wanda a gargajiyance su wanzaman Kano ba sa amfani da shi wajen yin kaciya (Hira da wanzami, Muhammad Hassuna Alewa).

Wannan ya tabbatar akwai bambancin kayayyakin amfani waxanda wanzamai suke amfani da su a wajen yin kaciya a gargajiyance a tsakanin wanzaman Hausawa Kanawa da wamzamai Larabawan garin Sebha.

### 9.2.5 Maganin Kaciya

Bayan an gama kaciya sai wanzami ya xauko askar yin kaciya ya yi alamar wurin da zai yanke da akaifa a wurin fatar farko ta kan azzakarin yaron, sannan sai ya sa askar ya yanke fatar ta farko ya kuma rage tsawon fata ta biyu, sai ya lanqwasa sauran fata ta biyu saman kan azzakarin yaron. Daga nan sai wanzamin ya tauna 'ya'yan bagaruwa ya  furza ruwan a wurin da ya yi yankan kaciyar. Dalilin amfani da 'ya'yan bagaruwa a wurin kaciya shi ne, don a yi gaggawar fitar da jini a kuma toshe hanyoyin da jinin ke fitowa kar ya wuce wuri, kuma tana taimaka wa idan an barbaxa magani a wurin kaciyar ya liqe. 'Ya'yan bagaruwa kuwa na taimakawa wajen saurin warkewar kaciya da kuma yin maganin kumburi ga kaciyar bayan an yi ta sannan idan an gama kaciya sai a bari sai jini ya gma fitowa sai a barbaxa maganin da zai sa kaciyar ta yi saurin warkewa. Maganin da wanzamai ke amfani da shi a wurin kaciya ir-iri ne, wato akwai bambanci tsakanin wannan wanzami da wancan, amma an fi amfani da sassaqen itacen qirya, da xakwara, da tsada da 'ya'yan itacen geza.

Ana haxa sassaqen itacen qirya da na xakwara, a haxa da sasseqen tsada ko 'ya'yan geza a daka sun sai a tankaxe a sami

gari mai launi. Irin wannan magani na kaciya idan mutum ya yi rauni da qarfe ida aka barbaxa masa a wurin raunin zai yi saurin warkewa. A wajen xibar maganin kaciya ba a amfani da qarfe domin sassaqo maganin, ana amfani da dutsi ne a riqa bugo sassaqen a samu wanda ake buqata. Dalilin shi ne, wai idan aka yi amfani da qarfe wajen xibar maganin ba zai yi tasiri sosai ba, wannan camfi ne kawai (Sallau, 2000:50).

A garin Sebha kuma idan an yi wa yaro kaciya za a xaure azzakarin da guntun yadi ko guntun rawani sai a bar kaciyar zuwa awa uku, daga nan sai a kwance xaurin da aka yi sai a samu man zaitun ko a samu qwai a shafa a kan azzakarin yaron da aka yi wa kaciya kuma da an shafa sai jini ya tsaya (Hira da Muhammad Hassuna Alewa).

Waxannan bayanai da suka gabata sun tabbatar akwai bambanci a vangaren ba wa xankaciya magani idan an yi masa kaciyar gargajiya a tsakanin wanzaman Hausawa Kanawa da wanzama Larabawan garin Sebha.

### 9.2.6 Bikin Kaciya

A qasar Hausa ana yin bikin kaciya iri biyu, akwai bikin da ake yi kafin a yi wa yaro kaciya, sannan akwai bikin da ake yi bayan an yi wa yaro kaciya.

Bikin da ake fara yi kafin a yi wa yaro kaciya a al’adar Hausawa shi ne idan za a yi wa yara kaciya iyayen yaran na aika wa danginsu da abokan arzikinsu na kusa da na nesa, su sanar da su cewa za a yi wa wane kaciya a ranar kaza. Idan ranar ta zo dukkan dangi na kusa da na nesa da abokan arziki sai su taru a gidan domin bikin kaciyar. Iyayen yaron za su yi abinci, a kuma daka gero a yi garin da za a yi kunun kanwa wanda za a ba yaran da aka yi wa kaciyar (Sallau, 2010:103).

A yayin gudanar da wannan bincike, an gano Hausawa Kanawa idan sun yi wa yaro kaciya, akan samu dangin mahaifan yaron da abokan arziqinsu da maqwabtansu su dinga shigowa gidan suna duba xankaciyar suna kawo masa hidima kamar kaji ko qwai ko kayan sawa ko kuma kuxi kamar dai yadda ake yi a kowanne biki na taya murna.

Su kuma Larabawan garin Sebha suna fara bikin kaciya ne ta hanyar uba (mahaifi) wanda kan je ya sanar da wanzami cewa zai yi wa xansa kaciya, daga nan sai su haxu su sa ranar da za a yi wa yaro kaciya, akan sa lokaci mai tsawo kamar sati xaya, sai uban yaro ya zo ya sanar wa mahaifiyar yaron cewa sun sa ranar da za a yi wa yaron kaciya, daga wannan sanarwar mahaifiyar yaron da

’yan’uwansa da maqwabta za su shiga shirye-shiryen fara bikin kaciya, wato a garin Sebha na qasar Libiya ana yin bikin kaciya ne kafin a yi kaciyar zuwa lokcin da aka yi kaciyar (Hira da Isa Muhammad Mabrok).

Ana fara bikin kaciya ne a garin Sebha ta hanyar kafa tuta fara a qofar gida. sannan ana fara bikin sosai ne saura kwana biyu a yi kaciyar, a ranar farko za a sa wa yaron da za a yi wa kaciya tufafin da aka tanada domin ya sa a ranar kaciya, sannan idan ana waxannan hidimomi na bikin kaciya, mata sukan haxu suna rera waqoqi musamman idan suna girka abincin da za a raba wa mutanen da suka zo taya su murnar bikin kaciya na yaronsu, ga irin waqoqin da suke yi:

فرشنا الحصيره وغربلنا التراب
حضرنا وجه محمد والشيطا ن غا ب

A sa tabarma a tanqaxe qasar nan,
Mun fara da ambaton sunan Annabi Muhammad (SAW),
Sai shaixan ya bar wajen.
(Hira da Amina Ali Muhammad)

Waxannan al’adu da aka yi bayanin yadda ake aiwatar da su sun tabbatar akwai bambance-bambance ta vangaren yadda ake

aiwatar da bikin kaciya a tsakanin Hausawa Kanawa da Larabawan garin Sebha na qasar Libya.

### 9.2.7 Wasu Al’adun Larabawan garin Sebha na Kaciya

Akwai wasu al’adun waxanda Larabawan garin Sebha suke yi a lokacin da suka yi wa yaro kaciya, amma Hausawa Kanawa ba sa yin su kwata-kwata waxannan al’adu su ne:

- Kafa tuta a qoar gida domin sanar wa mutane da cewa a wannan gidan za a yi wa yaro kaciya.
- Yi wa yaro carbin kuxi a rataya masa bayan an yi masa kaciya.

### 9.2.8 Wasu Al’adun Hausawa Kanawa na Kaciya

Akwai wasu al’adu waxanda wanzamai a garin Kano suke yi idan sun yi wa yaro kaciya, amma a garin Sebha ba a yin su kwata-kwata. Waxannan al’adu su ne:

- Amfani da karkiya
- Amfani da ’yarkara

## 9.3 Bambancin Kayayyakin da Wanzaman Gargajiya a Garin Kano da Garin Sebha a Libya Suke Amfani da su a Wajen yin Kaciya

Waxannan al’ummomi (Hausawa Kanawa da Larabawa Larabawan garin Sebha na qasar Libya) suna da kayayyakin aiwatar da kaciya a gargajiyance waxanda suka haxa da waxannan:

### 9.3.1 Askar da Hausawa Kanawa Suke yin Kaciya da ita

Aska da ake amfani da ita wajen yin aski qarama ce madaidaiciya, tsawonta bai kai kamu xaya ba. akwai bambanci tsakanin wadda ake askin jarirai da wadda ake yi wa manya aski. Ta askin jarirai ba ta kai girman wadda ake yi wa manya aski ba. da kuma askar aski ake amfani wajen yin kaciya, ana amfani ne da irin wadda ake yi wa manya aski wato mai kaifi domin a yi kaciya. A halin yanzu ana amfani da askar aski iri uku, akwai ta asali ta baqin qarfe, irin wannan aska ita wanzamai suka gaji amfani da ita, kuma maqeran Hausawa ne suke samar da ita ga wanzami. Aska ta biyu ita ce ta farin qarfe, wannan aska ta samu ne sakamkon samun kayayyakin da Turawa suka kawo a qasar Hausa. Ire-iren qarafan da ake amfani da su a wajen yin askar farin qarfe sun haxa da farin mustagadin babur ko farar banfa ta mota. Ita ma wannan aska maqeran Hausawa ne suke yin ta, bambancinta da ta farko shi ne launi, ita ta farko na baqa, ta farin qarfen kuma na fara.

Asakar aski ta uku ita ce ta Turawa. Irin wannan aska ta samu ne sakamkon zuwa aikin Hajji da Hausawa suke yi ire-iren waxannan asake na Turawa akwai waxanda ake sanya reza a cikinsu idan za a yi aski. Idan za a yi wa wani mutum kuma sai a sauya rezar. Akwai kuma wasu waxanda ba su da wurin sanya reza. Idan kaifinsu ya dakushe sai dai a kai wa maqera su sake qera su, a mayar da su irin na gargajiya na bacin qarfe (Sallau, 2010:47-48).

Wannan askar Hausawa Kanawa suna amfani da ita wajen yin kaciyar amma su mutanen da suke zaune a garin Sebha na qasar Libya ba sa amfani da ita.

### 9.3.2 Almakashin da Wanzaman Sebha ke Amfani da shi Wajen Yin Kaciya

A qasar Hausa ana amfani da almaqashi ne wajen gyara tsawon gemu da gashin baki da saje, ko kuma don yin saisaye. Shi ma almakashi akwai iri biyu. Na farko shi ne na gargajiya wanda maqeran gargajiya suka qera, amma a yanzu ba irin wannan almakashi da yawa.

Almakshi na biyu wanda wanzamai suke amfani da shi Turawa ne suka kawo shi qasar Hausa, a halin yanzu mafi yawanci wanzamani da shi suke amfani (Sallau, 2010:51-52).

Amma a yayin gudanar da wannan bincike, an fahimci wanzaman Kano suna amfani da almakashi ne wajen cire fatar da ta maqale ba ta fita ba, wasu kuma wanzaman da reza suke amfani a maimaikon amfani da almakashi.

Larabawan garin Sebha sune suke amfani da almakashi wajen yin kaciya, amma Hausawa ba sa amfani da almakashi wajen yin kaciya.

### 9.3.3 Karkiya Wadda Wanzaman Hausawa Kanawa Suke Amfani da ita a Wajen yin Kaciya a Gargajiyance

Karkiya karan dawa ne mai qwari ake samu a yanke tsawon misalin inci goma sha biyar zuwa inci ashirin. Ana amfani da karkiya ne ga yaron da aka yi wa kaciya lokacin da zai kwanta barci. Sai a xaura ta wurin cinyoyinsa domin maganin kar ya manta ya haxe qafafuwansa har matse kaciyar ya yi fami. Ita karkiya wasu wanzamai ne suke yanke ta su ba iyayen yaran da aka yi wa kaciya, wasu iyayen kuma kan yanke karkiya da kansu (Sallau, 2010: 56).

Larabawan garin Sebha na qasar Libya ba sa amfani da karkiya a wajen yin kaciya, wannan al’adar Hausawa ce.

### 9.3.4 ’Yarkara Wadda Wanzamai Hausawa Kanawa Suke Amfani da ita Wajen yin Kaciya a Gargajiyance.

’Yankara sallen karan dawa ne ake samu a yanke guntu-guntu. Ana samun sulle madaidaici domin yanke ’yankara. Ana yanka kowane guntu misalin tsawon inci xaya. Ana afmfani da ’yankara ne a wurin kaciya inda ake rarake uku a saka zare a cikin kowane sai a qulla zaren yadda ’yankaran za su yi kasuwa uku, daga nan sai a rataya wurin kaciya tsakanin azzakarin yaron da ’ya’yan golayensa. Amfanin ’yankara wurin kaciya shi ne su raba azzakarin yaron da ’ya’yan golayensa yadda kaciyar za ta riqa samun iska, kuma ba za ta riqa liqewa da ’ya’yan golayen ba. wannan na taimakawa wajen saurin warkewar kaciya. Wanzamin da ya yi kaciya ne ko yaransa kan yanka ’yankara (Sallau, 2010:55).

Mutanen da suke zaune a garin Sebha na qasar Libya ba sa amfani da ’yankara wajen yin kaciya, wannan al’adar Hausawa ce.

### 9.3.5 Fatar Washin Askar yin Kaciya a Kano

Sallau, (2010) ya bayyana cewa: “Fatar wasa asaken wanzamai fatar dabbobi ce ake samu daga wajen dukawa wadda aka jeme. Ana amfani da mai faxin misali inci xaya da rabi, tsawonta kuma misalin inci goma sha biyar zuwa ashirin. An fi

amfani da mai  kauri irin ta manyan dabbobi domin kuwa ta fi inganci da qara wa aska kaifi. Amfanin fatar washin asaken aski shi ne, idan aka wasa askar aski da dutse, kaifinta zai kai sosai ba sai an wasa da fata, ana shafa ruwa a fatar sai a bi da askar ana shafawa bisa fatar sannu a hankali., wannan ne zai daidaita kaifin askar yadda idan an zo yin aski askar za ta tuje gashin da sauqi. Mafi yawancin wanzamai na xaura fatar wasa asaken askin ga zabira daga gefe".

Wannan fatar ta washin aska ba a amfani da ita a wajen wasa al'makashin yin kaciya a Libya, Larabawan garin Sebha suna amfani da dutse ne wajen wasa almakashi a yayin yin kaciya.

### 9.3.6 Dutsen Washin Aska

Dutse washin asaken aski dutsi ne qaramin mai sulvi da ake amfani da shi domin yin washin asaken aski idan kaifinsu ya dakushe, wato kafifinsu ya ragu. Akwai duwatsu iri uku da ake amfani da su wajen wasa asaken aski. Na farko shi ne na gatarin aradu, wato dutsen da ke faxowa idan an yi tsawa lokacin ruwan damina, hanyar da ake bi domin samun dutsen gatarin aradu ita ce da zarar an yi tsawa, aka kuma yi dacen ganin wurin da ta faxa sai a yi gaggawa a je a zuba madara ko nonon shanu a wurin da tsawar ta faxi, inda an tona sai a

tarar da dutsen domin madarar ko nonon da aka zuba zai hana shi yin qasa da nisa. Dutse iri na biyu da ake amfani da shi domin washin asaken aski shi ne na qanqara mai sulvi wanda ake samu a kogi wurin da ke da duwatsu. Dutse na uku da ake amfani da shi domin washin asaken aski shi ne wanda Turawa suke yi domin washin alluran asibiti. Saboda yanayinsa ya yi kama da wanda ake washin asaken aski sai wanzamai suka riqa amfani da shi domin yin washin asaken aski (Salau, 2010: 49-50).

Su ma wanzaman da suke zaune a garin Sebha na qasar Libya suna amfani da ire-iren waxannan dutsunan wajen wasa almakashinsu na yin kaciya, wato dai dukkaninsu suna amfani da dutsen washi, sai dai bambancin yadda ake amfani da shi ne kawai, saboda su Hausawa Kanawa suna amfani da dutsen washi domin wasa aska, su kuma Larabawan Sebha suna amfani da shi ne wajen wasa almakashi.

A wannan babi an kawo bayanai a kan kamancin al'adun kaciya waxanda Hausawa Kanawa da Larabawan Sebha suke aiwatarwa a yayin kaciya kamar yadda ake aiwatar da kaciyar da kayan aiwatar da kaciyar da sutturar xankaciya da abincin xankaciya da yanayin jinyar xankaciya da bikin kaciya da waqoqin

xankaciya da kuma ire-iren kaciyar kanta duk an nuna kamancinsu da bambancinsu a tsakanin Hausawa Kanawa da Larabawan Sebha.

## BABI NA BIYAR

## 10.0 KAMMALAWA

A wannan babi, za a kawo bayanan kammalawa waxanda suka haxa da bayyana tasirin kaciyar zamani a kan ta gargajiya a tsakanin Hausawa Kanawa da Larabawan Sebha a Libya, sannan za aka kawo sakamkon bincike wato abubuwan da bincike ya gano da kuma bayyana shawarwari da wannan bincike zai bayar.

### 10.1 Tasirin Kaciyar Zamani a kan Al'adun Kaciya na Garin Kano a Nijeriya da Garin Sebha a Libiya

A garin Kano da garin Sebha, wannan bincike ya fahimci, an sami tasirin zamani a kan al'adunsu na kaciya saboda shigowar kaciyar da likitoci suke yi ta asibiti.

Sallau (2013: 197-1998) ya rawaito (Tuzin, 2006:2) yana cewa an gano tun cikin qarni na goma sha tara Turawan Ingilishi masu yawa suka fara yin wannan al'ada ta yin kaciya. Suna yin haka ne kuwa don dalili na kiwon lafiya. Wannan dalili ne ya sa suka fara yin kaciya a asibiti. Tun cikin qarni na goma sha tara ne likitoci suka kawo shawarar a riqa yin kaciya don tana taimaka wa wajen hana yaxuwar cututtuka musamman ire-iren waxanda aka xauka ta hanyar saduwa.

Haka kuma waxanda aka yi wa kaciya sun fi waxanda ba a yi wa ba sauqin jure buqatar saduwa da abokan saduwarsu. A asibiti ana yin kaciya ga jarirai da kuma qananan yara don qarin kula da lafiyarsu.

### 10.1.1 Kaciyar Asibiti

Ana yin wannan kaciya ne a asibiti, kuma ma su yinta likitoci ne waxanda suka qware a kan fixar fata.

A asibiti, idan za a yi kaciyar asibiti da farko, sai a yi wa yaron da za a yi wa kaciyar allurar da za ta kashe fatar wurin da za a yanke. Wannan ne zai sa a lokacin da za a yi kaciyar ba zai ji zafin yankan ba. Bayan an gama kaciyar, sai a shafa wa wurin da aka yanken magani, wanda a yanzu an fi yin amfani da aidin. Daga nan kuma sai a sanya auduga da bandeji a naxe kan azzakarin, wato wurin da aka yi yankan kaciyar.

Ana kuma yi wa yaron allurar riga-kafin kamuwa da ciwon sarqe haqora. Bayan wannan kuma ana ba yaron maganin rage raxaxi irin su *Paracetamol* (maganin ciwon kai da rage zafin ciwo) da ire-irensa waxanda za su taimaka masa ya ji sauqin zafi da raxaxin yankan da aka yi.

Haka kuma ana ba shi *Ampicillin* ko *Ampiclxo* (maganin kashe qwayoyin cuta) da *Vitamin C* (Maganin tsotse ruwan ciwo)

don su taimaka wa wurin da aka yi wankan ya yi saurin warkewa. Waxannan magunguna idan yaron da aka yi wa kaciyar jariri ne ko kuwa idan bai wuce shekara bakwai da haihuwa ba, ana ba da na ruwa don a riqa ba shi yana sha. Idan kuwa ya kai shekara bakwai da haihuwa ko wuce nan, ana ba da qwayoyin magungunan don a riqa ba shi yana sha. Malaman asibiti waxanda suka yi kaciyar ne suke ba da waxannan magunguna, kuma suna yin cikakken bayani dangane da yadda za a riqa ba yaran da aka yi wa kaciyar magungunan.

Bayan an yi kaciyar ana shawartar iyayen yaron da su riqa kawo shi asibiti duk bayan kwana biyu don a wanke masa a sake magani da auduga da bandeji. Za a yi ta yin haka har zuwa lokacin da yaron ya warke (Sallau, 2013: 197-198).

Wannan ya yi tasiri a wajen wanzamai, a inda su ma wanzaman gargajiya a yanzu musamman masu yin kaciyar sa wando suke amfani da paracetamol da allurar zalaten

Haka kuma Larabawan garin Sebha su ma a yanzu zamani ya yi tasiri a kansu, saboda mafi yawan Larabawan garin Sebha a yanzu sun fi yin kaciyar asibiti.

Saboda haka wani likita mai suna Dokta Abdulqadir ma'aikacin asibiti mai suna "Fazzan" ya bayyana min cewa ana yin kaciyar asibiti ne a garin Sebha saboda waxannan abubuwan:

- Tsabtar jiki wato sauqaqa da tsarkake azzakarin mutum
- Kiyaye mutum daga wasu cututtuka da fitsari ke haddasa su, ire-iren waxannan cututtuka su ke jawo ciwon qoda.
- Kare mutum daga kamuwa da cutttuka waxanda ake samu a yayin saduwa da mace (saduwar aure).
- Kaciya tana rage kamuwa da cutar kansa, sanan tana taimakawa wajen gamsar da mace a lokacin saduwa.

Haka kuma "Walid" ya bayyana yadda ake kaciya a likitance kamar haka:

> "Za a kwantar da yaro sannan a riqe hannayensa ko a xaure hannayensa da qafafunsa, bayan haka sai a wanke masa azzakarinsa da ko'ina a gefensa, daga nan sai likita ya yi masa allurar kashe zafi ko qaiqaiyi, ana amfani da magani irin biyu wajen kashe zafi a yayin kaciya, wato ko a yi amfani da magani na shafawa ko a yi amfani da allura, bayan likita ya sa maganin kashe zafi sai ya ja fatar azzakarin, ya xaure ta da wani maxauri na musamman wanda aka yi shi da roba bayan haka sai likita ya yi amfani da almakashi ya cire (yanke) fatar da ke lulluve da azzakarin, daga nan sai likita ya shafa magani a jikin kaciyar sannan ya xaure ta da wani yadi na musamman (bandeji) duk wannan aikin yana faruwa ne cikin mintina goma[5]".

[5] Hira da Dakta Walid Gemin, likita a asibitin da ke garin Sebha na qasar Libya.

Rakiya (2015) ta rawaito cewa an yi hira da wata likita a gidan rediyon Faransa mai suna Fatima a inda ta ce: “Yi wa mata kaciya babban kuskure ne, sannan ta ba da misalin bambancin da ke tsakanin macen da aka yi wa kaciya da wacce ba a yi ma ta ba, ta bayyana cewa kaciyar namiji ta fi ta mace daraja, in da ita kaciyarta take rage mata sha’awa da jindaxi, wadda ba a yi wa kaciyar ba tafi wadda aka yi mata daraja a wurin mijinta”.

### 10.1.2 Magungunan da Likitoci Suke Bayarwa Idan an yi Kaciya a Asibiti

Sallau (2013:198) ya kawo magungunan likita ne a vangaren kaciya kamar haka:

- Allurar riga-kafin kamuwa da ciwon sarqe haqora.
- Maganin ciwon kai da zazzavi (Paracetamol).
- Maganin kamewar ciwo da kashe cututtuka (Ampicillin ko Ampiclox).
- Maganin qara kuzari (Vitamin C)

Haka kuma Dakta Fatima Hassan Likita a asibitin da ke garin Kano ta bayyana min cewa “Magunguna da ake ba wa xankaciya da waxanda ake yi masa kafin kaciya da bayan kaciya a likitance su ne kamar haka:

- Zylocain (Maganin kashe zafin ciwo)
- Adnanaline injection (Allurar tsayar da jini)

- Ampiclox (Maganin kashe qwayoyin cuta)
- Bnustan N (Maganin ciwon jiki)
- Vitamin C (Magani tsotse ruwan ciwo)

Sannan kuma Dokta Abdulqadir Usman likita a asibitin "Fazzan" da ke garin Sebha na qasar Libya ya bayyana min cewa magungunan da ake ba wa xankaciya da wanda ake yi masa kafin kaciya da bayan kaciya suke kamar haka (magungunan likita wanda ake ba xankaciya a asibiti):

- Medical kuhuyl (Maganin wanke ciwo)
- Paracetamol (Maganin ciwon kai da rage zafin ciwo)
- Fucidin (Man shafawa a kan kaciya domin ya kawar da cututtuka)
- Amoxicilin (Maganin kashe qwayoyin cuta)

## 10.2 Abubuwan da Bincike ya Gano

Ba shakka wannan bincike da aka gabatar ya gano waxansu abubuwa kamar haka:

An gano Hausawa Kanawa suna yi wa yaransu kaciya a shekara bakwai da tara a gargajiyance, amma ba sa yi a shekara takwas saboda sun camfa idan aka yi wa yaro kaciya a shekara takwas yana kamuwa da cuta (Sallau, 2013: sh. 153). Amma a yayin gudanar da wannan bincike an gano Hausawa Kanawa sun watsar

da wannan al'adar wato suna yi wa yaransu kaciya daga haihuwa zuwa shekara tara a duk sanda suka ga dama.

Sannan an gano cewa mutanen garin Sebha suna kafa tuta a qofar gidansu domin su sanar wa da jama'a cewa za su yi wa xansu kaciya. Haka kuma wannan bincike an gano cewa Larabawan garin Sebha suna da al'adar yi wa yaro (xankaciya) carbin kuxi a rataya masa a wuya a yayin aiwatar da kaciya (Hira da Amina Ali Muhammad).

Har ila yau wannan bincike ya gano cewa a qasar Hausa wanzami ne yake yin kaciya haka ma a garin Sebha sai dai yawanci wanzaman garin Sebha suna zama mahaddata *Alqur'ani*.

Wannan bincike ya gano cewa a qasar Hausa ana yin bikin kaciya ne iri biyu kafin da bayan an warke a gargajiyance wato bikin warkewar kaciya (Sallau, 2010; sh. 103) amma a garin Sebha ana fara bikin kaciya ne tun kafin a yi kaciyar zuwa yinta da bayan an warke (Hira da A'isha Abdussalam).

Haka kuma wannan bincike da na gudanar ya gano cewa Larabawan garin Sebha suna sama wa xankaciya sabon tufafi domin fitar kaciyar amma a garin Kano ba dole ne a sama wa xankaciya sabon tufafi ba ana iya yi masa kaciya da tsofaffin kayansa.

Sannan wannan bincike da na gudanar ya gano ana yin waqoqin tsokanar xankaciya a yayin gudanar da bikin kaciya a garin Kano, amma a garin Sebha na qasar Libya kuma mata dangin xankaciyar su ne suke yin waxannan waqoqi, a inda a garin Kano makaxa da maroqa ne ke yin waqoqi da kirare-kirare a lokacin bukin kaciya, sai dai waqoqin zolayar xankaciya a garin Kano an gano yayyensa da sakwanninsa da abokansa da kakanninsa da duk wani abokin wasansa ne suke yi masa.

A wannan bincike an gano wasu al'adun kaciya waxanda Larabawa Larabawan garin Sebha da Hausawa Kanawa suke aiwatarwa kuma suka yi kama da juna waxanda suka haxa da waxannan:

i. A garin Kano idan an yi wa yaro kaciya 'yan'uwa da maqwabta suna kawo gudummawa a ba wa xankaciya musamman kaji ko nama ko sababbun kaya ko kuma a ba wa mahaifansa kuxi a matsayin gudummawa da taya murna, haka ma Larabawan garin Sebha su ma idan mutum ya yi wa xansa kaciya 'yan'uwansa da maqwabta kan kawo gudummawa a ba wa xankaciya kamar yadda ake yi a garin Kano na Nijeriya.

ii. Wannan bincike ya gano a al'adar Larabawan garin Sebha na qasar Libya sukan gayyato wanzami tun ranar Alhamis ya zo ya kwana, sannan ana yin kaciya ranar Alhamis da saf ko juma'a, ko

ranar Asabar da yamma. Amma a al’adar Hausawa Kanawa ana yi wa yaro kaciya a ranar Juma’a a gargajiyance, sai dai a yanzu a kowace rana ana iya yi.

A wannan bincike an gano waxansu al’adun kaciya waxanda Hausawa Kanawa da Larabawa Larabawan garin Sebha na qasar Libya suke gudanarwa a yayin kaciya amma suka bambanta da al’adun kowaxanne daga cikinsu. Misali:

A qasar Hausa ciki har da garin Kano sun amince su yi wa yaransu kaciya a lokacin sanyi wannan al’ada ce wadda har yanzu Hausawa Kanawa suna aiwatar da ita, suna yin kaciya da sanyi ne domin sun amince kaciyar ta fi warkewa da wuri a lokacin sanyi amma su kuwa Larabawan garin Sebha na qasar Libya a kowane lokaci suka ga dama suna yi wa yaransu kaciya. Wato sukan yi wa yaro kaciya a lokacin zafi ko lokacin damina ko kuma lokacin sanyi savanin Hausawa Kanawa waxanda suka zavi lokacin sanyi a matsayin lokacin da za su yi wa ’ya’yansu kaciya.

### 10.3 Shawarwarin Bincike

A wannan bincike an nazarci al’adun kaciya waxanda Hausawa Kanawa suke aiwatarwa a lokacin kaciya da bayan kammaluwar kaciya (warkewar kaciya), sannan an nazarci al’adun

da Larabawan garin Sebha na qasar Libya suke aiwatarwa a sanadiyar yi wa ’ya’yansu kaciya, an kawo kamanci da bambnacin na waxannan al’adu da waxannan al’ummomi (Hausawa Kanawa) da Larabawa Larabawan garin Sebha suke gudanarwa a lokacin yi wa ’ya’yansu kaciya.

Bayan kammaluwar wannan bincike akwai shawarwari da wannan nazari zai bayar ga masu nazari a nan gaba domin a faxaxa binicke a kan wanzanci da abubuwan da wanzamai suke yi a sana’arsu musamman kaciya a nan gaba, daga cikin shawarwari da wannan bincike zai bayar akwai:

- Yana da kyau a nan gaba a nazarci basirar xaixaikun wanzamai xaya bayan xaya, domin ta haka ne za a gane hikimar kowane wanzami wajen iya aikinsa na wanzanci.

- Zai yi kyau a nan gaba a nazarci kwatancin ayyukan wanzanci na wani wanzami guda xaya Bakano da wani wanzamin mazaunin garin Sebha, musamman a kowane gari a xauki wani wanzamin da ya shahara kamar sarkin wanzamai kamar yadda qasar Hausa suke da shi.

- Abu ne mai matuqar muhimmanci a nan gaba wani masani ko xalibin ilimin a nan gaba ya nazarci ayyukan wanzamai wanda

ba kaciya ba kamar aski da sauransu, kuma ida an samu dama zai yi kyau a nazarci kwatancin ayyukan wanzanci na aski a tsakanin Hausawa Kanawa da Larabawan garin Sebha a inda binciken zai kalli aski kawai kamar yadda wannan aiki ya kalli ko in ce ya nazarci kaciya kawai.

A wannan babi, an kawo bayanai a kan kammalawar wannan nazari ta hanyar fito da tasirin da kaciyar asibiti take da shi a kan kaciyar gargajiya a garin Kano da Sebha. Sannan an fito da abubuwa da dama waxanda wannan nazari ya gano, tare da bayyana shawarwarin da wannan nazari ya bayar domin qara faxaxa bincike a wannan fage na al’adun al’umomi.

# MANAZARTA


Abu Yazid (2009). ومضات من التراث الليبي*Wamaxat min alturat allibi.* Baiba: Alsharka Al'amah lil warq

Abu-kuresha, (2002). تأملات في الواقع الإجتماعي المصري Ta'annlat fi alwaqi alijtema'a alsre, Aswan, markazalmahrusalbuhutwa altadrib wa alnashir.

Adamu, M.T. (1997). *Asalin Hausawa da harshensu.* Kano: Xan Sarkin Kura Publishers.

Ahmad, M. (2013). *Al'adun mutane, Maroco:* Al'xabi'a Al'nashri Wal Tauzil.

Alhamani, (1987). الأزياء الشعبية والثقافية في سوريا (Al'zya Alsha'abiya wa taqalidahafi suraya), dimashiq, manshurta wazarat altaqafa.

Al-kashat, (2006). التراث الشعبي العربي الليبي (Alturat alsha'abi Alarabi Allibe) Bangazi, Al'ajna Alsha'ibiya Al'amalltakafa.

Almajir, T.S. (2009). "Tasirin Zamani a kan Rayuwar Hausawa matasa a Kano". Kundin Digiri na Biyu. Kano: Jami'ar Bayero, Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya.

Al-Samarra'i, (2004). التقاليد والعادات الشعبية (Altaqalid wa Al'adat Al'dimashqiya). Seriya: Al'awa'il wa Al-tauzi'a.

Babale, S. (2008). "Barkwanci Tsakanin Wasu Masu Sana'o'in Gargajiya a Qasar Hausa". Kundin Digiri na Farko. Zaria: Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya da Al'adun Afirika. Jami'ar Ahmadu Bello.

Bagafar, (1971). رباط الولايا (Rebat alwalaya). Jidda, dar Albalad.

Bin Araifa, (2006). تاريخ فزان الثقافي والإجتماعي (Tarih fazzan altaqafi wa al’ijtima’i). sebha. Markaz Alwatanillmahfuxat wa aldirrasat altarihiya.

C.N.H.N. (2006) *Qamusun Hausa*. Zaria: N.N.P.C.

Doguwa, I.H. (2013). “Kwatancin Al’adun Haihuwa na Hausawa da na Kurama a Kudancin Kano da Gabashin Zazzau”. Kundin Digiri na Biyu. Zaria: Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya da Al’adun Afirika. Jami’ar Ahmadu Bello.

Dokaji, A.A. (1978). *Kano ta dabo cigari*. Zaria: N.N.P.C.

Durumin’iya, (2006). *Tasirin Kimiyy da Qrere-Qeren Zamani kan San’ao’in Hausa na Gargajiya*. Kabs Print Services, Kano, Nigeria.

Gixaxo, S.M. (1998). “Asali da Al’adun Miyawa” Kundin Digiri na Farko. Zaria: Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya da Al’adun Afirika. Jami’ar Ahmadu Bello.

Gunim, (2005). العادات والتقاليد في دلتا مص (Al’adat wa taqalid fi dalta masar). Alqahira, Ainkdresat wa albuhut al’insaniya wa al’ijtama’iya.

Gusau, S.M. (2015). *Mazhabobin ra’i da tarke a adabi da al’adu na Hausa*. Kano: Centurey Research and Publishing Ltd.

Halima, H.A. (2012). “Tasirin al’adun Hausawa a kan Ibira a Kano a yau”. Kundin Digiri na Biyu. Kano: Jami’ar Bayero, Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya.

http://changingminds.org/explanations/culture/hall culture.com

Ibrahim, M.S. (1982). “Dangantakar al’ada da addini tasirin musulunci kan rayuwar Hausawa ta gargajiya”. Kundin gidiri na biyu. Kano: sashen Koyar da Harsunan Nijeriya.

Madabo, M.H. (1979). *Ciniki da sana’oi a qasar Hausa.* Lagos: Thomas Nelson Nigerian Limited.

Madauci da wasu, (1968). *Hausa Customs*. Zaria: Nothern Nigerian Publishing Company Ltd.

Magarabi, (1982). ملامح الحياة الإجتماعية في القرن العشر الهجري (Malamah Alhaya Al’ijtima’iya fi alqarin ashar Ilhijra). Jidda: dar Jidda llxiba’a wa Alnashir.

Mohammed, (1998). ذاكرة قرية (*Dakirat Qarya*. Alsharka Al’ama kwaraq wa Alxiba’a). Sebha, Libya.

Musa, (2008). الأدب الشعبي وثقافة المجتمع (“Al’adab Al’sha’abi wa Al’taqafat Al’mujtama”). Cairo: Huquq Alxaba’a wa Al’nashir Dar Al’mahrusa.

Nash, N. (2009). سبها-برقن وثائق وأسماء (*Sebha wabirqin wataiqwa asma’a*) Sebha: Saut at taba wa alnashir watarjimu wa’atiqtibas.

Rafi’u, (1981). مكة في القرن الرابع عشر (Makka a cikin qarni na sha huxu (14) Alhizri). Makka Almuharrama, dar Makkallxiba’a wa Alnashir wa Altawzi.

Rakiya, A. (2015). “Shin Bahaushe ya karvi al’adar kaciyar ‘ya’ya mata ne? In haka ne wace irin rawa take takawa a rayuwar ‘ya mace”. Takarda wadda aka gabatar a ajin digiri na biyu a qarqashin kwas mai lamba HAU 8830. Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Kano: Jami’ar Bayero.

Sallau (2000). “Wanzanci: Matsayinsa na al’ada da sana’a a qasar Hausa”. Kundin digiri na biyu. Kano: Sashen Koyar da Harsunan Nijeirya. Jami’ar Bayero.

Sallau, (2009). Sana’ar wanzanci da sauye, sauye zamani jiya da yau. Kundin digiri na uku. Kano: Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami’ar Bayero.

Sallau, (2010). Wanzanci da muhimmancinsa ga rayuwar Hausawa, Kaduna: M.A. Naji’u Professional Pinters.

Sallau, (2013). *Wanzanci da Sauye-Saauyen Zamani*. Ahmadu Bello University Press, Zaria, Nigeria.

Sallau, B.A. (2010). *Magani a sha a yi wanka a buwaya.* Kaduna: M.A. Naji’u Professional Printed.

Satatima, I.G. (2012). “Patronage of ‘sa wando’ circumcision practice in the metropolist of Kano: traditional or modern?” maqalat a cikin *Hemispheres studies on cutlures and societies,* Warsaw: Institute of Mediterrance and Oriental Cultures, Polish Academy of Science.

Sutton, J.E. (1979). Towards aless orthodiyo, History of Hausaland a cikin Journal of African History, Vol. 20.

Shanono, G.A. (2006). Al’adun Shekara-Shekara a Qasar Hausa”. Kundin Digiri na Farko”. Zaria: Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya da Al’adun Afirika. Jami’ar Ahmadu Bello.

Taha, (2009). الطقوس والمعتقدات الشعبية والاجتماعية في الأدب (“Al-tuqus wa Al-mutaqadat Al’sha’abiya wa Al-ijtima’iya fi Al’adab”). Kundin Digiri na Biyu. Falasxin: Jami’ar Al’najah Al’Waxaiyya.

Tanko, A. A. (2000). “Tasirin harshe da al’adun Hausawa a kan Gwarawa”. Kundin gidiri na biyu. Kano: Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya.

Yahaya, M. (2014). “Kimiyya da fasahar Bahaushe kafin zuwan Turawa qasar Hausa”. Kundin digiri na xaya. Zariya: Sashen Koyar da Harsunan Afrika, Jami’ar Ahmadu Bello.

Yakubu, D. (2008). “Qaramin Qamus na Kevavvun Kalmomin Wanzanci”. Kundin Digiri na Farko. Zaria: Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya da Al’adun Afirika. Jami’ar Ahmadu Bello.

## RATAYE NA XAYA
## HIRARRAKI

**Mutanen da aka yi Hira da su**
Amina Ali Mohammad
‘Yar shekara saba’in da huxu (74)
Ranar 22/2/2016
A garin Sebha

Isa Mohammad, xan shekara sittin da biyar (65)
Mazaunin garin Sebha, Libya
Ranar 12/3/2016

A’isha Abdussalam, ’yar shekara saba’in da huxu (74)
A garin Sebha, Libya
Ranar 18/3/2016

Dr. Walid Eanim
Xan shekara hamsin da takwai (58)
Likita da yake aiki a asibitin Al’afiyah,
A garin Sebha, Libya
Ranar 20/3/2016

Dokta Fatima Hassan
‘Yar shekara arba’in da xaya (41)
Likita a asibitin Hasiya Bayero, Kano
Ranar 19/08/2017

Dokta Abulqadir Osman
Xan shekara hamsin da huxu (54)
Likita a sibitin Fazzan da ke garin Sebha, Libya
Ranar 10/02/2016

Musa Zakariya
Xan shekara arba’in da huxu (44)
Mazaunin unguwar Rijiyar Zaki a Kano
Ranar 25/02/2017

Hassan Abubakar
Xan shekara sittin da bakwai (67)
Wanzami mazaunin Unguwar Rijiyar Zaki, Kano
Ranar 25/02/2017

Yahya Wanzami
Xan shekara arba’in da biyu (42)
Mazaunin garin Katsina
Ranar 30/03/2017

Salmanu Muktar
Xan shekara hamsin da tara (59)
Wanzami mazaunin Unguwar Xanbare, Kano
Ranar 04/04/2017

Mohammad Hasuna Alewa
Xan shekara sittin da biyu (62)
Wanzami mazaunin garin Sebha
Ranar 25/02/2016

**Tattaunawa da Wanzamai**

1. Muhammad Hassuna Alewa, a garin Sebha na qasar Libya
2. Hassan Abubakar Shu'aibu, xan shekara Sittin da biyar, mazaunin Unguwar Rijiyar Zaki gaban tasha.
3. Yahya Wanzami Jihar Katsina.
4. Salmanu Mukhtar Unguwar Xanbare Kano.
5. Salmanu Abdullah mazauna unguwar Xorayi

**Tattaunawa da Masana da Manazarta**

- Dokta Muhamamd Sa'id na sashen harshen Larabci a Jami'ar Sebha ta qasar Libya,
- Dokta Aliyu Burhana na Sashen Tarihi a jami'ar Sebha ta qasar Libya,
- Dokta Kassim Bilal na sashen Hausa a jami'ar Sebha ta qasar Libya.
- Farfesa Isa Mukhtar Jami'ar Bayero, Kano.
- Farfesa Sa'idu Muhamamd Gusau Jami'ar Bayero, Kano.
- Dokta Ibrahim Garba Satatima Jami'ar Bayero, Kano.
- Dokta Aliyu Mu'azu Jami'ar Bayero, Kano.
- Dokta Muhammad Tahar Adamu Jami'ar Bayero, Kano.
- Dokta Bashir Sallau Safana Jami'ar Umaru Musa da ke Katsina
- Malam Kamilu Xahiru Gwammaja, Babban xakin karatu na Jami'ar Bayero, Kano.

**Tattaunawa da Likitoci**

- Dokata Abdulqadir Usman Abdulqadir a asibitin Fazzan a Sebha
- Dokta Wa'il Ganim asibitin al'afiyah a Sebha
- Fatima Hassan asibitin Hasiya Bayero a Kano.

**Tattaunawa da Tsofaffi**

- Isha Muhammad Mabruk xan shekara saba'in da uku (73) a garin Sebha,
- Kabiru Sani Auwalu, xan shekaru sittin da tara (69) mazaunin Unguwar Rijiyar Zakik kusa da Masallaci
- A'isha Abdussalam 'yar shekara saba'in da biyar (75) a garin Sebha,
- Ali Abdurrahman xan shekara tamanin da biyu (82) a garin Sebha.
- Hadiza Alhaji Magaji 'yar shekara sittin da takwas (68) a garin Kano.
- Ali Dauda xan shekara saba'in da shida (76) a garin Kano.
- Rabi'u Ahmad Barkum xan shekara sittin da biyar (65), ma'aikaci a babban xakin karatu a Jami'ar Bayero, a vangaren Larabci.
- Fatima Abdussalam Kalid 'yar shekara saba'in da takwas (78) a Sebha.

**RATAYE NA BIYU**

**KAYAYYAKIN DA WANZAMAI KE AMFANI DA SU DON YIN KACIYA A GARIN KANO**



Aska



Karkiya



Fatar Washin Aska



Dutsen Washin Aska



Zabira



Tankolo

Tankolo ’yar jaka ce wadda dukawa suke xinkawa da fatar akuya ko tunkiya domin wanzamai su riqa sanya askar aski xaya ko kuma babba wadda za a sanya asaken aski masu yawa (Sallau, 2010: 58)

## RATAYE NA UKU
## Yadda Hausawa Kanawa Suke yin Kaciya















































Hotunan mai Bincike da Wanzamai Guda Biyu
Mazauna Garin Kano




Malam Salmanu Abdullahi Mazaunin Unguwar Xorayi
a Jihar Kano Tare da Mai Bincike Hassan Mahdi Jibril




Malam Hassan Abubakar wanzami mazaunin unguwar
Rijiyar Zaki a jihar Kano tare da mai bincike
Hassan Mahdi Jibril

**RATAYE NA HUXU**

**Hotunan Kayayyakin Aikin Wanzami Abubuwa na Al’adun Kaciya a Garin Sebha na Qasar Libya**



Almakashi



Reza



Yaro an rataya masa carbin kuxi bayan an yi masa kaciya


Wanzami yana riqe da yaron da zai yi wa kaciya


Xankaciya da shigar kaciya wato hular kaciya
da tufafin kaciya a garin Sebha



Rigar fitar kaciya a garin Sebha



Xankaciya ya sa hular kaciya a Garin Sebha

**RATAYE NA BIYAR**
**Yadda Wanzami yake Gudanar Kaciyar a Garin Sebha na Libya**



















































Malam Muhammad Hasuna wazami mazaunin unguwar Altanawiya ta garin Sebha na Libya tare da mai bincike Hassan Mahdi Jibril